Mika ma Bintu fanke daya tayi kato cikin jin dadi ta amsa tace nagode Hurriya ,shiru Hurriya tayi tana kallon yadda Bintu ke cin panke a hankali ta kara kiran mai fanken cikin muryarta Mai dadi kara mika mashi kudin tayi tace ya bata na dari guda biyu ya kara bata mika ma Bintu tayi amsa tayi tace inason ki Hurriya sannan ta rinka cin fanken kamar bata taba cin abinci duniya ba Girgiza kai Hurriya tayi Bintu ce tace ma Hurriya kalli abinda dogarawa can keyi Hurriya mun bani Hurriya kallon saitin da dogarawan suke tayi taga sun sanya sun jera layi layin maza daban na mata daban Hurriya batasan ma cewar akwai mata ba sai yanzu da tagansu jere a layi kallon Bintu tayi tace tare dawa kukazo Bintu da har ta fara kuka ta kalli Hurriya tace da wadancan azzaluman dogarawan daga kai Hurriya tayi tace ya akayi kika biyosu kuka Bintu ta fara tace muna zaune a tsakar gida saiga kawar Larai nusaiba ta shigo daki suka shi itafa Larai nusaiba tace ga yan masarautar Qamar nan sunzo zasu dauki ma'aikata da bayi. Shine tace kawai ta tura ni aiki ba bauta ba suna biyan kudi Sosai kuma  ita za'a rinka bama kudin  ina labe inajin su har nusaiba ta fito kallona tayi tace kuma naji ance sun fison mata kyawawa kuma kinga Bintu ba daga baya ba sai Larai tayi dariya tace kedai bari ba karamin taimakona kikayi ba nusaiba zan yadda kwallan mangwaro In huta da kuda gshi kuma Abun riba biyu dariya kawai nusaiba tayi  tace ai kin yanman albashin nata ko?? Larai tayi dariya tace abinda yafi albashi ma don bakaramin taimakona kikayi ba suka kalli Bintu Larai ai nasan ubanta baida matsala nusaiba kenan ya bani matsala ma yaga ikon Allah

Bintu ta kalli Hurriya dake kallonta shine fa suka sanya na biyo dogarawan Hurriya daga mata kai kawai tayi ta juya saitin dogarawan tana kallon tsantsar zalincin da sukeyi Maza da matan dake jere a layi ake cajewa duk abinda aka ganka dashi sai a amshe har cikin riga suke lalubar matan cikin tsantsar zalinci abun gwanin ban takaici Hurriya a hankali ta zaro sauran kudinta dake cikin aljihu ta sanya su cikin safarta gyara safar tayi yadda ba wanda zaiga abinda ke a cikin kafarta cikin sa'a kuma ba wanda ya kula da lokacin da ta dauke kudin Shaho ne da yake kusa da Kumurci suna zaune suna kallon duk abinda ake don kamar sune manya kaga wata yarinya Mai kyau kamar ita tayi kanta nifa bantaba ganin mai kyau irinta ba dogon gashinta ya bani mamaki nace anya bahaushiya ce kuwa ko yanayin shigarta kadai zata nuna maka haka saidai fa kaga yadda take kallonmu girgiza kanshi yayi Kumurci nifa idanuwanta tsoro suke bani Kumurci yarinyar can fa na cikin hadari saboda karnukan

dake masarautar mu fa sunada yawa gashi ba babba ba yaro don ko nifa sai na lasa yana karasawa da lashe baki Kumurci wani kallon banza yayi mishi wanda ke hade da gargadi shiru shaho yayi cikin ranshi yace wallahi sai na lasa ai kaima nasan manufar ka munafuki

Wani dogari ne ya kalli saitin dasu Hurriya suke kai tsinanu yan gidan matsiyata kuzo nan Hurriya ko motsi batayi ba Bintu tace mata Hurriya ki taso don Allah mu tafi kadasu dake mu banza Hurriya tayi da ita don maganar duniya taki ta tashi su Kumurci da shaho duka suna kallon abinda ke faruwa Bintu zuwa tayi ta shiga layi kwalla na zubo mata dogarin kau cikin hasala yazo saitin Hurriya kallon shi tayi cikin ido shine ke sanya hannunshi acikin rigar mata tashi tayi tsaye tace da uwarka da ubanka sune manyan matsiyata da har suka haifo wanda baisan dajar halitar mata ba kaskantarce kuma duka halayenka ke defining kaskanci Bullock wata muguwar ashariya shaho ya saki yace kaga wannan yarinyar Kumurci shuru yayi kowa ma shiru yayi yana jira yaga abinda zai faru Azuciye dogarin ya daga bulalar ya zuba mata a baya,mata da mazan wurin duka tsigar jikinsu tashi tayi suka juya itakam Hurriya kwalla ce ta zubo mata abinda ta dade batayi ba a rayuwarta wato kuka ta kasance a kullum rayuwarta ita Mai kukan zuci ce har tana jin dama zata iya irin kukan da Bintu keyi kilan ta samu sanyi ko yayane a ranta bulalar da yayi mata har cikin kanta taji azaba matuka wanda ta durkusa kasa hawaye na zubowa Daga hannunshi yayi da niyyar kara dukanta Kumurci ya rike hannun yace ya isa haka Garba ajiye hannunshi yayi ba don yaso ba sannan Kumurci ya yace tayi shiru sannan yace  ki iya bakin ki idan ba haka ba to kina hanyar da bazata bullar dake ba don masarautar Qamar sai yayi murmushin mugunta Hurriya tana durkushe a hankali ta shafo hawayen don ta tabbatar da idan nagaske ne kallon hawayen tayi fa dagaske sune tasan ba lallai ta kara maimaita irin wannan kukan ba saboda yau sau biyu tayi kuka sannan ta kasance zuciyar ta Mai rauni ce saidai idan kaganta zakayi mamakin minene ya sauyata har haka da ba abinda yake girgiza ta ko ya bata mamaki kuma fa rashin ganin mutumcin kowa duk girman ka Daidai take da kowa don ko yaro yajefeta da magana sai ta maida mashi martani da wadda tafi tashi zafi shine kawai abinda ke sanya ta magana ko sai kuma idan tana tare da Bintu don Bintu zata iya awa tana mata magana baifi ta bata amsa daya ba saboda miskilancin ta Bintu har ta saba.

Kumurci kallonta yake saboda yasan akwai matsala a masarautar nan idan har Hurriya ta shige ta don ya lura bazata taba saukar da kanta kasa ba don haka yake tunanin hanya daya zai bi don tasamu barin masarautar batare da ansamu matsala ba shine yace baiwa ya samota kuma yaroki alfarmar ta zama Baiwa hakimi shine kawai mafita anma ta cigaba da haka baisan a hannun wazata mutu ba don princes da princesses din masarautar nan basu da imani ga kuma dayar matsalar don Kumurci yayi nadamar tahowa da Hurriya don yasan ba karamar wuya zatasha ba don ko yaran sarki kadai sun isheta don sun tsani wani yafisu kyau duk da daman masarautar kyawawa akafi kaiwa saidai ba wanda san dalili to zai iya rantsewa tunda ake kai kyawawan mata a masarautar baitaba ganin Mai kyaun wannan yarinyar ba don su kansu yaran mai martaba sai sun raina kansu.

Kallo daya zakayi mata kasan ta jigata ba karamar jigatuwa ba ma don wandon dake jikinta duk yayi datti fuskar ta kuma duk ta kumbura ga babu annuri kwata kwata saida fa annurin kyanta nan don sai salki takeyi Kumurci yace ki tashi ki shiga mota mu tafi yanzu bada hargagi yayi mata maganar ba don zuciyar shi ta dan karye kadan Kallonshi tayi da idanunta masu kyau da wani kaifi Kumurci ya daga mata kai tare da fatar kada tayi kafiya irin wadda tayi dazu.

A hankali take takawa amman zaka iya hango zallar mulki dake cikin tafiyar tata har ta shiga motar a hankali Kumurci girgiza kai yayi don ya hango kurar dake tafe da ita saidai Allah ya kyauta don aikin gama ya riga ya gama.

Bintu kam lokacin da ta koma layi cikin sa’a ba ba wanda ya  lalubeta saboda hankalin kowa da ya koma kan Hurriya tanajin su karime dake gabanta cikin layi suna dariya suna cewa Allah ya kara sa’ade ce tace kinsan dadin da nikeji yadda ake bugun Hurriya karime tayi murmushi tace naki kika sani ni yarinya ta dade tana bani haushi shegiya ga isa ga iko sai kace wata shegiya sa’ade tace bata da mutunci Hurriya kinga cin mutunci da tayi ma mahaifina kuwa harda watsa mashi man awara akafa bayan tagama zazzageshi cikin mutane karime yo naji maganar tana yawo agari ki bari idan munje mu hade kai mu ci ubanta don ni ta dade tana bani haushi don kiga duk anguwar mu ace mazan ita kadai suke kallo to yanzu lokacin mune idan munje muyi maganin karuwa Mai ma  maza jiki.

Bintu duk tanajinsu don harda kukan ta wurin da suka ce mata karuwa don tasan karya sukeyi Allah ya saka maki Hurriya inji Bintu ta fada cikin ranta.

Hurriya da ta koma wurin zamanta ta jinginar da kanta jikin window tana rufe idonta saidai kyarma kawai takeyi tana harhade hakoranta ga sanyi da ya isheta dankwalin da ta daura ta rufe gashinta dashi ta koma ta kwanta saidai sanyi ya matsa mata don bata daina jinshi ba ledar kayanta dake gabanta ta jawo saboda Asabe hada kyautar doguwar hijab tayi mata don lokacin har ta kawo zaure Asabe ta kwala mata kira a hankali asabe ta mika sabuwar hijab doguwa maroon tace Hurriya ko bazaki sanya ki fito ba ai nasan kina sallah to ki rinka sallah da ita inda so samu ne ki rinka fita da ita sai kuma ta tabe baki tace nasan yaudarar kaina nike ba inda zaki da ita tace Hurriya ki godema Allah don wallahi inasonki duk wanda yaji nayi kyauta sai ya kusa suma saboda mamaki kindai sanni da san kudin tsiya Hurriya batace mata komai ba har tagama maganar ta sai Hurriya ta mika mata ledar alamun ta sanya Asabe kam sauri ta dauko ta sanya Hurriya ta tafi ba godiya bare sallama.

Hijabin ta lalubo ta sanya ta dunkune kanta ciki a hankali bacci ya dauketa.

Sosai suka sha tafiya har suka iso Babbar masarautar Qamar bata sani ba don kowa ya fita a motar ya barta Kumurci ne ya kula da babu ita don har anfara kada kyayoyinsu Kumurci ya bude motar yazo inda take bacci da yake bai san sunanta ba don haka yace ke ki tashi mun iso shiru Hurriya tayi saida yayi mata magana kusan sau uku sannan ta bude idon wadanda sukayi mata nauyi Sosai har lokacin tana jin jikinta na kwankwatsa Kumurci yace ki fito munzo kuma kada kiyi ma mutane kafiya da rashin kunya don kece  zaki sha wahala Hurriya da batajin karfin jikinta kwata kwata don ko yadda take numfashi zaka iya lura tashi tayi ta rungumo kayanta saidai tana tafiya biyu ta sake su Kumurci da yayi gaba yaji karar kayan da tasaki don haka ya juyo ya kalleta sannan ya daukar mata kayan suka fita duk da suna zuwa ana sallahr magriba don duhu har yafara Bayyana Amman bazaka iya gane cewa rana ce ko dare ba saboda haske da ya wadaci ko ina a babbar masarautar Qamar Masarautar kanta abun kallo ce girmanta gari guda ne tunda ga floor din dake kasan masarautar da ginin da akayi mutum zai gane cewar masarauta ce maiji da tsantsar dukiya kuma da karfin mulki .saidai Hurriya ba Abu daya wanda ya burgeta don kallo daya tayi ma komai wanda bata kara kallon wani Abu ba

Su Bintu da su karime kam Murna sukeyi kamar su ciji duwawunsu basu san masarautar Qamar, bawuri bane da ya kamata ace ya burgesu ba ko su kasance masu farin ciki Don masarauta ce wadda take cike da tsantsar zalinci da rashin imani.Kusan duk wadanda sukazo dasu sakin baki suke suna kallon ko ina.

Tasa keyarsu akayi ana bugunsu kamar tumaki suka shigo ciki inda ba abinda kake gani sai dagorawa dake tsaitsaye fuskar su hade kamar zasu je yakin basasa hannunsu daya narka narkan bulali Dayan kuma hannu dogayen bindigu kowane,Ba wanda bai firgita ba da ganin wadanan dogarawan don fuskar su babu alamun sassauci

Hurriya da da kyar take tafiya saboda zazzabin da take wani bakin dogari ne ya sakar mata bulala wadda saura kadan ta fadi da kyar ta cigaba da tafiya

Kumurci da yaga banda dukansu ba abinda akeyi yayi dauriya yace basu bane bayin ,Dukansu tsaya sukayi suna kallon Kumurci saboda dokar masarautar ce duk wanda yafi ka matsayi dole kabi umarninshi kuma duk abinda zaiyi ba wanda ya isa ya dakatar dashi saidai idan har akwai wanda yafika matsayi zai iya hanaka to

Kallon Kumurci suke da idanunsu masu sawa mutum ya shiga zullumi Kumurci da duk ya tsure yace Allah ya gafarce ku Kumurci yana Neman sassauci. Saminu ne ya iso don kusan duk yafi su matsayi ya kallesu yace lapya?cike da rusunawa ya fara mashi bayanin abinda ya faru wani kallo Saminu yayi masu wanda nan take suka bar wurin ya kalli Kumurci yace ka shiga dasu ciki kuma duk wanda ya tareka kace ni na baka umarni shiga dasu daga ciki sannan ya bar wurin.

Kallon su shaho yayi da yan matan da suka taho dasu da mazan,saitin Hurriya ya kalla yaga tanajan numfashi da kyar ta hade gwiwar ta da kanta,tunda aka tsaidasu ta kwanta Kumurci ba karamin dadi yaji ba lokacin da yaganta da hijab ya tabbata da ace ba hijab jikinta da yanzu wani ya shiga dakinshi da ita gashinta kuma da tuni an datse saidai cikin ikon Allah ta rufe duka jikinta harda kusan rabin fuskarta.

Tafiya sukayi inda suka kara nitsa kansu cikin masarautar sakin baki kusan Dukansu sukayi don haduwar masarautar tafi bayyana yanzu akan wurin da suka baro a baya kuyangu ne da bayi da hadimai wadanda basu da iyaka kowa da hidimar da yake kuma kusan kowa da kalar uniform din dake jikinshi wasu green and red wasu green and orange wasu green and yellow wasu green and blue.

Su karime kam yau sun samu Tv don suna kashe ma kwarkwatar idon su haka suka rinka tafiya don daga inda suka baro zuwa inda sukazo yanzu tafiya ce Mai wani irin nisa don dukansu sun gaji shaho yace a kira uwale uwar bayi ta raba masu aiki tun yanzu Kumurci ya daure yace ai kasan ka'idar abun dole sai sunkai gobe saboda jakadiya tana shiyar uwargijiyar ta yanzu to bari na nemo uwar bayi Shaho ya tafi don nemo uwar bayi ba tare da wani bata lokaci ba sai gashi sunzo fuskar ta ba annuri bare fara'a Kumurci ne ya gaisheta cike da girmamawa ya mikasu wurinta Kumurci Kallon Hurriya data gama galabaita yayi cikin aljihun shi ya fiddo paracetamol da ibuprofen ya bata kin karba tayi don kusan sau uku yana mata magana ta amsa Amman ko kallon inda yake batayi ba bare har ya sanya ran zata amsa a ranshi yace zaki sha wuya ne a masarautar nan don duk kafiyar ki sai kin ajiyeta don dubunki ma sunyi sun gama

Kumurci ya dora mata maganin saman hijab sannan ya juya ya bar wurin,su karime kam sai kallon yadda ta zukana sukayi she looks so pale and weak yanayin da ba wanda ya taba ganin ta dashi tunda take rayuwarta she's always strong and fierce don haka Dukansu da mamakin yadda take suke sai Abu na biyu da ba wanda ya taba ganin ta dashi wato hijab tunda duk wanda ya kwana ya tashi ba wanda ya taba ganin Hurriya da hijab a unguwar su shiyasa suke kallonta da mamaki uwar bayi ce ta kallesu tace wai Lapia kukayi tsaye kallon mazan tayi tace zata kira halliru ya shigar dasu ta kalli su Bintu tace su tafi.

[12/02, 4:53 PM] Khadyn Sp: Masarautar Qamar

By Khadija (KMU)

Page 11&12

Uwar Bayi ce gaba suna biye da ita tafiya sukayi Mai nisan gaske kafin su iso wani babban gini kallon wurin su Bintu suka rinkayi ita dai Hurriya ta kosa ta kwanta don kiris ya rage mata ta daina tafiya saboda kasusuwan ta da suke kwankwatsa kusan dukan su itace karshe wurin tafiya uwar bayi ce ta shiga dasu cikin ginin wanda yake da bangare iri da iri a ciki

Kuyangi ne kowace da uniform dinta suna hidimar su tunda suka shigo yan matan dake zaune suke binsu da wani irin kallo Hansa'u ta tabo barira tace kinga mun samu sabbin zubi yau Barira da take kallon Ko wanne a cikin su daya bayan daya cikin izza da takama tace uwar Bayi daga ina aka samo mana sabbin tumakai su sa'ade da karime duk suka bude baki Hurriya da tanajin sun saidai ta kanta takeyi Uwar bayi kam batace komai ba ta wuce suka bi bayanta

Hansa'u ta kalli barira tace kinga yan mata tsala tsala nifa harna hango wacce tayiman Barira yadda take zaka dauka wata diyar sarkice saidai kawai saboda tafi su mukami kuma tanada saurayi a cikin dogarawan don haka take baza nata mulkin a inda ya kamata cikin izza da mulki tace kudai bi a hankali kada wata acikin ku ta shiga gonata sannan ta tashi tana wani juyi wanda kamar dagan gan takeyinshi su Hansa'u Dukansu biyota sukai abayanta.

Uwar Bayi wani babban daki ta kaisu wanda yake da Bayi kusan duka manya mata ma ko ina shimfede da katifa kowa kallonsu yakeyi da tausayi don ace yara da kuriciyar su sunzo azzalumar masarautar nan don neman abun duniya but basusan cewar lalatar rayuwar su sukazo yi ba don a masarautar tasu miye ba a aikatawa na kazanta babu shi Duk abinda baida kyau shi akeyi ga zalunci.

Uwar Bayi ta kalli yan matan da tazo dasu tace to nidai ga makwanci don haka ku nemi inda zaku kwanta kafin gobe tayi a rarraba maku wurin bacci Dukansu godiya sukayi mata sukaje neman wanda zai taimaka yadan rabasu kafin zuwa goben da tace.

Hurriya kam tana duke bata motsa ba  bare tayi i tunanin tafiya Uwar bayi ta kalleta tace kiyi maza kije ki nemi wurin kwana ko ki kwana a kasa tunda ba'a gidanku kike ba Hurriya dagowa tayi ta kalleta wani irin kwarjini tayima Uwar bayi Uwar bayi batace komai ba ta tabe baki ta fita.

Bintu kam har tasamu wurin kwana matar Mai kirki kamar ma budurwa ce ita ta kara  Bintu kuma katifar katuwa ce zata ishesu su biyu Tunawa Bintu tayi da Hurriya don ba taganta ba tunda suka iso a hankali ta fara o dubata kafin ta hango ta zaune a tsakiyar dakin cikin sanyi sai kallonta akeyi da sauri Bintu ta nufi inda take tace Hurriya a hankali ta dago idonta da sukayi jajir ta zuba ma Bintu hankali tashe tace Hurriya mike damunki baki lafiyane? Subahanallah ta dora hannunta saman goshin Hurriya & tureta tayi da sauran karfin daya rage mata tace How dare you touch my Royal Body maganar na fita da karkarwa saboda kyarmar da takeyi Bintu tace kiyi hakuri don Allah hankalina ne ya tashi dana ganki haka Bintu tasan cewar Hurriya na bala'in sonta duk da cewar bata nunawa amman idan Bintu na mata labari hankalin ta duka take bata ko Daga yanayinta zakasan tanajin dadin ko wani irin labari Bintu ta bata kuma tasan har abada bazata samu kawa irin Hurriya ba don ako da wani lokaci itace Mai tsaya mata tsayin daka a rayuwarta ta kwatar mata yanci a wurin kishiyar uwa da shikanshi mahaifinta don ba wanda baisan irin muzgunawar da suke mata saidai Hurriya ba ruwanta haka zatazo tazage su tass kuma tayi masu babban kashedi na idan suka kara matsa mata zata dauko masu hukuma kuma sunsan halinta saboda ta taba dauko ma Larai da baban Bintu yayi magana tace a hada dashi saida Bintu tayi sati daya a wurinta lokacin abinci duk idan zasu ci sai ta tambayi Bintu mizasu siyo kuma duk abinda Bintu ta gani tanaso sai ta siya mata shi wani lokacin da kanta take tambayar Bintu Abu kaza yayi maki idan tace Eh zata sai mata shi kamar batasan darajar kudinta ba kuma idan har Bintu tazo bata kara kwana a katifa sai a kasa saboda Hurriya ba wanda ya isa ya taba koda hannunta don tasan wannan halin nata duk wanda yayi gigin taba ta sai ta sauke mashi mari Bintu ma kafin su saba kusan sau uku tana Marinta saboda yawan kai hannu jikinta daga bayane saidai ta tureta tayi mata kallon kada ta kara.

Kallon Hurriya tayi tace mata sanyi ke shigar ki muje ki kwanta banza tayi da ita Bintu kuka ta fashe dashi tana ma Hurriya magiya ta tashi sanyi Amman ina kusan duka mutanen dakin kallonsu suke Bintu kam da taga Hurriya taki tashi sai ta kwanta kasan siminti tana kuka tace mata don Allah ki tashi idan har baki tashi ba nima anan zan kwana Hurriya kallonta tayi cikin muryarta mai cike da rashin karfi tace Bintu ki shekara a kasa idan kin tashi Bintu da tasan wacece Hurriya tayi mata sanin da ba wanda yayi mata shi don tabbas Hurriya dagaske take ta shekara kwance a siminti itadai batasan mi ya faru a rayuwar Hurriya ba daya maidata haka kamar dutsi

Fashewa da kuka Bintu ta karayi sannan ta tashi tanayi mata magiya kallon yanayin Hurriya tayi wanda banda hakoranta dasuke gabgab ba abinda sukeyi wani kuka ta kara fashewa dashi mai tsuma zuciya ta fara hadata da Allah mutane duka kallonsu sukeyi suna mamakin irin son da Bintu keyi ma Hurriya ita kuma Hurriya ta kafe kamar kafurar  farko sa'ade tace kibar shegiyar ta mutu kowa ma ya huta kafura Mai bakin hali Karime tayi caraf tace tun ba aje ko ina ba karshen karuwa yazo namu dai muyi kallo duk jiji da kan mutum dole ya ajiye shi don ubanshi zaici yayi anan.

Hurriya duk tanajinsu duk da ciki ciki sukayi maganar ta yadda bazata iyaji ba ,saidai sunanta fa Hurriya Faisait Hamood. Magana daga nesa komin kasa da murya da mutum zaiyi sai taji ta kamar gizo gizo haka take Allah ya bata kunnuwa kamar ba irin na mutane ba saboda kaifin ji da suke dashi.

A hankali ta fara wani irin tari harda sarkewa salati Bintu ta rinkayi tana kuka da tarin ya tsaya ba abinda take sai karkarwa Bintu a hankali ta rage tsawonta tana kuka tace ki taimakeni Hurriya ba

kanki zaki taimaka ba Hurriya tunda nike baki taba musu da duk abinda nace inaso ba sai kinyi mani shi don Allah ki taimakeni ki tashi ba don halina ba Hurriya kallon Bintu tayi da idanunta masu kyau saidai sun rikida sun koma jajawur saboda azaba don har jijiyoyin idonta ana gani

Hurriya tashi tayi a hankali ta fara takawa saidai kafafunta banda kyarma ba abinda sukeyi Bintu ta dafata saboda kada ta fadi tureta tayi da sauran karfin da ya rage mata har Bintu na faduwa kasa tana binta da wani kallon cikin muryar ta da ta shake tace kina hauka ne ,Bintu kuka take tana girgiza kanta tace Aa to sai ta kasa maganar tana Neman faduwa Bintu da sauri tazo ta tarbeta kada tafadi kasa daga Hannunta Hurriya tayi da basu da karfi sosai ta wanka mata mari tana kallon Bintu da sai kuka take sannan ta sake ta

Mutane kallon dramar kawai suke wasu lokaci daya Tsanar Hurriya ta kamasu saboda rashin mutuncinta suna jin tausayin Bintu wasu kuma zaginsu kawai suke suna cewa marar sa mutunci zasu zubda hali daga zuwansu duk munsan ma'anar abinda kukeyi hmm mutane sun iya judging din abinda bashi bane Har sun manta da cewar yau su Hurriya da Bintu suka zo bare suyi irin hallayar da suke magana.

Hurriya da kanta ta taka sukazo har inda Bintu ta samu wurin kwana Bintu kam dadi ta rinka ji don har ta goge hawayen ta.

Habiba kallo daya tayi ma Hurriya ta washe mata baki tace sannu yanmata Hurriya ko kallon inda take batayi ba bare ta sanya ran zatayi mata magana

Bintu kallon Hurriya tayi tace bari tayo alwala, waje ta fita sannan ta dawo  ta gyara hijab dinta ta fara rama sallolinta har tagama Hurriya idonta a rumtse yake don ta jinginar da kanta jikin katifa.

Bintu bayan tagama addu'arta ta kalli Hurriya tace in samo maki abinci Hurriya daga mata kai tayi alamar Eh Kallon habiba Bintu tayi tace ina zan samo mata abinci Habiba tace muje in raka ki kitchen ki amso naku abincin to inji Bintu don haka tabi bayan Habiba suna tafiya akan hanya sai habiba ta dan wuce Bintu itakuma Bintu tana ta tunani tana tafiya.

Habiba juyowa tayi baya sai taga Bintu na tafiya kamar wacce zata fadi dawowa tayi ta rike mata hannu gam tace kina tunaninta ko ?kada ki wani damu zaki samu wadanda suka fita komai a masarautar nan wacce zata kula dake kuma ta soki sai ta farayi mata tafiyar tsutaa acikin hannu tace Ko nima idan kika bani dama zan maye maki gurbinta Sai ta tsunkuli Bintu a waist dinta tana kashe mata ido daya itadai Bintu kallon ta kawai takeyi ba tace uffan ba don batasan inda zancen nata ya dosa ba kallon habiba tayi tace muje ko naga lokaci na tafiya Dariya habiba tayi tace gaskiya kinason wannan yar tawalwalar ki nima inason inga ana kula dani haka shiyasa nike kaunar ki don daga gani kinada kulawa ko kukan da kikayi mata kadai ya isa ya nuna hakan

Gaskiya inasonki nagode kawai Bintu tace sannan tace muyi sauri kada tayi bacci murmushi habiba tayi ta rike mata hannu suka fara tafiya da fan dan sauri sauri itadai Bintu tanajin yadda take mata tafiyar tsutsa da hannu har suka kai babban kitchen din da ake dafa ma bayi da kuyangi da masu aiki abinci ba'a wani hantare su ba saboda sanin sune sabbin ma'aikatan da suka zo don suna bukatar Abinci don habiba tayi masu bayani

Plate biyu aka basu cike da tuwo habiba ta amsa ita kuma Bintu tayi tsaye tana kallo ana miko mata plate din Habiba ta kalleta tace ki amsa mana bata fuska Bintu tayi tace ba shinkafa ne? Kallonta mai bada abinci take da mamaki tace ke yar Gidan maysiyata ki amsa idan ba haka in maida ki kwana da yunwa shegiya har MU zakiyi ma iyayi alhalin agidan ku ba lallai kina samun kalar shi ba Habiba ta mintsinota Bintu ba domin ranta ba haka ta amshin abincin saboda tasan ba lalle cewar taci tuwon ba

Suna zuwa suka ga Hurriya ta kara dukunkune wa don ta kara makurewa wuri daya kamar da alama sanyi takeji Bintu tace Hurriya ki tashi ki ci abinci A hankali ta bude fuskarta tana kallon Bintu da take kuka a hankali tace ya akayi kuma?Share Hawayen ta Bintu tayi tace Hurriya don Allah ki ci abinci kada ki ce bazaki ci ba akwai nisa fa inda muka amso kuma kinga baki lafiya tana sakin baki kamar karamar yarinya Dan tsotsar bakinta Hurriya tayi kamar daman sararta ce ta daga mata kai

Cike da jin dadi Bintu ta miko mata tuwon Habiba dai tana kallon ikon Allah kwano ta samu ta debo ruwa sannan taba Hurriya ta wanke Hannunta ta fara cin abincin a hankali ta dan ci ba laifi tanajin ta koshi ta ture plate din ta kalli Bintu ,da sauri ta kara miko mata kwano ta zuba mata ruwa ta wanke hannunta Habiba cike da kaudi da son ta samu shiga tace Hurriya ga magani kisha na ciwon kaine Da zazzabi Hurriya ko kallon inda Habiba take batayi ba don a hankali ta sanya hannuta cikin hijab aljihun wandonta anan ta fito da magungunan da Kumurci ya bata hannun Habiba har lokacin yana tsaye tana bata magani cikin muryar ta da take da alamun rashin lafiya tace Bintu bani Ruwa.

Da sauri Bintu ta bata ruwa ta shanye maganinta kallon habiba Bintu tayi tace kiyi hakuri tana da wuyar sabo ne Amman tana da kirki zaku saba In Sha Allah .Bari in tafi in samo wurin kwana sai Hurriya ta kwanta tare dake,Habiba murmushi tayi cikin yanga tace yi zamanki ki kula da abarki ba mai takura maku nizaje inda nima za’a kula dani,dadi sosai Bintu taji ta farayi mata godiya don tasan idan har Hurriya ta kwanta Habiba ta kwanta kusa da ita kilan za’a iya tashi aga habiba kwance saboda irin dukan da Hurriya zatayi mata kuma itakanta Bintu bazata taba bari ta kwana kasa ba saboda sanyi.

Habiba ta fita tace matsiyata kuma ashe kunsan harka muje zuwa ta nufi dakin Su Hansa’u  Aiko tana shigowa sukazo suka zagayeta sukace mata habiba ya bakin nan nagansu tsalatsala guda habiba tayi tace ayiri to ku kwantar da hankalin ku don ba wata wahala da zamusha wannan karan wurin jawo hankalinsu tace ai yan gidan matsiyatan suma duk sun san harka don wadda na bama makwanci ma baki gansu ba kamar zasu cinye juna nan ta kwashe labari ta basu tass dariya suka rinkayi suka ce gobe zasu zo ta nuna masu yan matan suna fata ma Allah ya sanya akawosu dakin Barira duka tana jinsu Amman batace komai ba don shiru tayi.

Bintu kallon Hurriya tayi da ta fara gyangyadi tace ki kwanta ni zan kwanta kasa daga mata kai Hurriya tayi ta kwanta dukun kune cikin hijab dinta bacci ne mai wahala ya dauketa Bintu kam tagumi ta buga tana kallon Hurriya don ta hango wahalar da zatasha a masarautar nan don Hurriya bata durkusa ma wada sadai da alama waddanin sunyi yawa a masarautar kuma wahala zata sha don ko bata durkusa ma ma’aikata ba ai akwai ubannin gidansu da dole suyi masu biyyaya tana fatar dai Allah yasa kada su sha wahala don ganin Hurriya tana wahala tamkar itace take wahalar bazata iya dauka ba.

Murmushi tayi ganin Hurriya ta  tsotsi bakinta sai kuma ta turo bakin tana bata fuska alamar shagwaba magana tayi da wani yaren Bintu da take kallonta taji tana magana tana bata fuska da wani yaren da bata taba ji ba

Don tasan yaren dai gaskiya babu kalar shi a Nigeria

Kallon kyaun hallitar fuskarta takeyi yadda tayi ma fuskarta kamar wata baby magana takeyi cike da shagwaba murmushi Bintu tayi tace naga ranar da Hurriya zata daina daure fuskarta tana shagwaba haka tabb akwai ruwa da kankara ranar.

Bintu bacci ta faraji don Haka ta kalli Hurriya ganin ta dukunkune wuri daya kuma ga space nan da yawa don haka ta raba gefenta ta kwanta nesa sosai da ita don kada cikin bacci Hurriya taji ta a kusa da ita ta tureta

Addu’a tayi sannan ta runtse idonta bacci mai cike da gajiya ya dauketa .

Karfe bakwai  Bintu ta tashi har lokacin Hurriya bata tashi daga bacci ba ta makara don haka agurguje ta kama ruwa hade da alwala tazo tayi sallah .Tana gama Sallah taje inda taga sauran yan uwanta karime tayi ma magana tayi banza da ita don haka tayi ma uwale magana tace miye akeyi anan uwale tace zamu tafi ne za'a araba mana aiki bata ida magana ba saiga Uwar bayi tazo Kallonsu tayi tace saifa kun kula kubi a hankali kuskure daya a masarautar nan zai iya zamar mutum babban kalubale a rayuwarta, kowa amsa mata yayi sannan suka bi bayanta tafiya sukayi Mai nisa sannan suka iso katon wuri inda mazan dasuka zo duk sunja layi suma layi sukaja suna kallon kyawu da tsarin masarautar da babu wani Abuna more rayuwa da bai wadace ta ba.

Kwance take a lallausar katifa wani Abu dake gefenta kamar wasan yara ya fara kara bude idonta tayi masu cike da bacci kokarin komawa take Amman karar ta hana ta karar wayarta ta hade da karar abunda yaketa wakar yaran tsoki taja tana maganganu da kuma mamakin wani marar sa'a ne ya tada ta daga bacci Amman bari Taga kowaye tana jawo wayar wani call din na kara shigo mata kallon wayar tayi da wani bacin Rai cikin muryar ta maidadi tace oh my God sannan ta ziro dogayen kafafunta wani Abu ta latsa saiga kuyangi guda Biyu sun shigo suna dukar da kansu kasa sannan cike da mugun girmamawa sukace Allah ya taimake ki Allah ya kara maki Nasara Allah yasa wannan Rana tazamar maki Ranar farin ciki da Albarka Batace masu kala ba sai da tagama Shan kamshinta sannan ta kallesu Dukansu ba wanda baisan ma'anar kallon da tayi masu ba don haka da sauri daya daga cikin kuyangar ta shiga toilet dinta ta hada mata ruwa Daidai yadda tasan tana amfani dashi kullum ta zuba mata flowers masu kamshin dadi ta wanke mata brush ta sanya mata macline Mai kamshi ta fito tana durkusawa tace Allah ya taimaki Batatuma Angama

Dayar da take tsaye wacce har ta dauko pink towel dan dora mata towel din tayi  sannan ta zame mata rigar tareda rumtse idonta  ta yadda kada a samu matsala taga wata siffa ta jikinta cewa tayi ya isa don Haka ta juya Neela ta ida daura towel dinta ta shiga toilet din saida ta farayin brush tadan shafa wasu abubuwa na skin care sannan ta shiga bahon da aka hada mata ruwan wanka lumshe idonta tayi tadan fara wasa da ruwan saida ta dauki mintina kafin tayi applying showe gel dinta mai sanyi dadi ta wanke jikinta tass sannan ta fito

[12/02, 4:53 PM] Khadyn Sp: Masarautar Qamar

By Khadija (KMU)

Page 13&14

A hankali ta fito daga toilet din tana fitar da wani kamshi har tazo tsakiyar dakin da angyara shi tass kamar ba'a taba kwanciya ba vanity table ta zauna tana kallon kanta olive skin dinta sai glowing takeyi ringing din wayarta ne yayi kara wanda tasan ba kowa bace face kilan mahaifiyarta a hankali ta tashi kamar wadda batasan taka kasa saidai ba kasa bace batason takawa tsantsar sarautar dake yawo a jikinta ne   bata fuska tayi ganin Mai kiranta kin dauka tayi har ta tsinke karar wayarta ne ta karayin kara dauka tayi ta kanga a kunnenta muryar mai dadi da sautin amo tana ratsa dakin don da tsiwa take maganarta liya wai lapia kike kirana kamar wadda ta ci maki bashi daga dayan Bangaren liya wadda tagama shiryawa tace I just missed my twin sister i decided to check on her ko nayi laifi ne Neela takirata da karfi tace liya da bacin rai a muryarta dariya liya tayi tace wallahi kiyi sauri ki fito ko In kira basai na fada ba kindai san sauran su idan na kirashi Neela tayi sauri ta dafe zuciyarta tace bansan kalar wasannan dariya liya tayi tace Don't forget to wear green palazzo and white shirt

Tun jiya na sanya akawo maki kayan so kiyi sauri kinsan mu suke jira tunda Mai Martaba da kanshi yace Aikinmu ne Neela da take saurarenta cike da taikaici tace I know I know go to hell Liya I hate you liya dariya tayi tace I love you Neela kashe wayarta tayi . Twin sister dinta kenan she always gets on her Nerves shiryawa tayi cikin kayan da  Liya tace akawo mata tun jiya wandon palazzo ne na prada da wata rigar gucci da takalma da scarf

Inner wears ta sanya sannan ta fesa turaruka masu tsananin tsada ta shirya cikin kayan wadanda elegance dinsu sun fito ko ta ina kayan ba karamin kyau sukayi mata ba don dan karamin scarf ta daura kusan duka rabin gashinta ya zuba a baya sai kamshin mai masu dadi takeyi Kallon kanta tayi A madubi sannan taga yadda tayi kyau murmushi tayi wanda ya fito mata da dimples dinta she's proud of her beauty don masarautar tasu sai kana da kyau za'a san da existance dinka shiyasa subira tayi masu fintinkau saboda tsanin kyau da mulkinta Tunawa kawai da tayi da ita taji zuciyar ta na tashi bloddy Hell tace saboda tasan ta kusa dawowa ba dadewa Neela tace koda yake da da yanzu ba dayaba ,ba zata iya daukar iskancin subira ba zuciyarta ce tace kullum sai kince da da yanzu ba daya ba Amman kullum dayane saboda ba abinda kuke iyawa a gaban yarinya mai jin kan tsiya.

Tsoki tayi ta fito katon parlon ta wanda yake cike da abubuwan more Rayuwa tunda ga floor din parlon da chandeliers din da suke à sama wanda suke bama ko ina wani irin haske wall bracket din kuma masu wani irin designs na royalty masu bala'in kyau fitilu ne ko ta ina haske kam har zai iyayi ma mutum illa saboda parlon baida wani hayaniya sosai don American parlor ne ko royal chairs babu kujerun l-shape designs masu kyau

Tana fitowa kuyangin Dukansu suka dukar da kai kujerar dining daya daga cikin su ta ja mata ta zauna sai kuma daya daga cikinsu tazo da sauri ta zuba mata Irish da liver sauce sai coffee cewa tayi su ta zataci abinci don duk sunyi mata tsaye da sauri kuyangin suka fita waje suna jiranta tagama cin abinci ta take hankalin kwance saidai wayarta na hannunta tana duba wani abu a Instagram kara taji wadda karar ta kusa firgitata,Neela da tasan ba wanda zaiyi hakan sai liya don waye ya isa bama wanda ya isa liya janye plate din Neela tayi ta faracin chips din tace shey you're here enjoying your breakfast nikuma banci komai ba haba Neela tana maganar tana dafe zuciyarta sannan tace Baki da kirki kallo daya zakayi Neela kasan ta gaji da halin yar Uwarta wadda kammanin su daya don idan zaka tsaya kana kallon su baka isa ka gane daya acikinsu ba,saboda kamanninsu. liya cin cips din take harda muguntta while Neela kallonta kawai takeyi har ta cinye sannan ta dauki coffee din dake gefenta ta shanye dariya tayi tace yanzu naji Daidai tashi mu tafi Neela hararta tayi tace liya daga yau kada ki kara shigo mani chamber dafe zuciyarta tayi sai ta bata fuska tace haba my twin kin sanya an raba mana chamber yanzu kuma so kike in daina shigowa chamber kwata kwata tana dafata tsoki Neela tayi ta ture ta dariya liya tayi tace muje

Tare suka jero suna tafiya Dukansu kuyangin a bayansu wasu kuma a gabansu olive skin dinsu sai shining yake with the help of the sun don Duk bala'inka baka isa kace ga Neela ba ,ko liya saboda tsananin kammannisu moto ci aka bude ma kowace a cikinsu sannan suka shiga baya Daidai inda su Bintu da sauran mutanen da suka zo dasu suka tsaya Bintu da sun kusa awa uku suna jira Dukansu sun gaji ga yunwar da sukeji kamar mi saidai hankalin ta baki daya yana wurin Hurriya da har yanzu bata ganta a wurin ba.

Kallon princesses guda biyu masu kama daya sukeyi su Dukansu kamar kauyawa maza da matan duka kallonsu sukeyi kyau, siga, gayu ,sa'ar rayuwa da mulki kawai suke gani lahaula wala kuwatta illah Billah kawai Bintu take cewa kamar rana haka suka fito don sun haske ko ina don kowa su yake kallo

Kuyangin a gaba da bayansu sukuma a tsakiya Har sukazo inda aka tanadar masu su kadai don su zauna kujerun kansu abin kallone

Su Bintu natsuwa sukai wurin ya dauki wani irin shiru liya da Neela kallon kowa sukeyi da isa kuma da sarauta da idanunsu masu kaifi

Kuyangin kuma duk sun dukar da kansu a tsaye magana liya tayi da kuyangar dake kusa da ita

Ita kuma ta isar da abinda tace ga uban kuyangu da bayi.

Hurriya tun dazu ta tashi lokacin da ta tashi sai taga ba kowa a dakin don haka ta fito ganin kuyangu tayi duk suna ta hidimar su kowa da abinda yakeyi wanka takeson tayi don jikinta duk yayi tsami bata matsa daga inda take ba tsaye saiga Kumurci yazo da ledar kayanta da mamaki yake kallonta Saboda yaga sauran yan uwanta wurin da suke jiran Gimbiya Batatuma da Gimbiya shawata cike da mamaki yace ya akayi Bakije ba banza tayi dashi,Hurriya kamar bada ita yake magana saida ta jima sannan cikin muryar ta Mai tsanani dadi tace bani kayana ta ida maganar tana tsotsar bakinta kadan

Kumurci kallonta yake yana kara tasbihi aranshi yarinyar Allah yayi mata tsananin kyau ga wani uban kwarjini da take dashi ita kam da tasan yadda daurewar fuska keyi mata kyau data rage daurewa tana dariya kilan mazan masarautar hankalin su bazai dauku da kyawunta ba

Kallon kayan jikinta yayi tun na jiya ne wanda yaganta dasu ba hijab ko dankwali babu don duka gashin yayi baya ya sauka a bayanta tsaki Hurriya tayi tace malam ka samu Tv ne?kumurci da yadan daburce cike da borin kunya yace ga kayanki Hurriya kallon kayan tayi sannan tace ka ajiye zan dauka da mamaki yake kallonta don ba'a taba yi mashi irin haka ba Hurriya kam ta rungume hannunta tana kallonshi ido cikin ido kwarjin tayi mashi sosai don haka ya janye idonshi akwai abinda yakeson gaya mata Amman bai iyawa saboda yadda bakinshi yayi mashi nauyi juyawa yayi ya tafi ita kuma Hurriya tayi tsoki ta kalli wata kuyanga sannan tace ina zata tayi wanki Kuyangar sakin baki tayi tana kallonta don sauran kadan ta ruga saboda kyauwunta da gashinta kallonta kuyangar kawai takeyi Hurriya da ranta ya fara baci don ta tsani kallo itama cike da rainin wayau tace wai Tv na Zamar maki ne hajajju Aa baiwar Allah kinada kyau ina jiye maki tsoro ne ga kuma kina da gashi kuma naga shigar kamar bata musulma ba tsoki Hurriya tayi tace akwai wata doka ta sanya kayane? Girgiza mata kai kuyangar Tayi tace ina guje maki karnunkan masarautar nan ne maza da mata

Hurriya tace kinsan fundamental Human right?girgiza kai tayi Hurriya akwai Right of choice yanzu idan naga dama zanyi yawo yadda nakeso kuma ba wanda ya isa yayi depriving right dina so shiga zanyi wadda nikeso hakajju iyakar ki kallo

Kuyangar tace iyakata kallo kuwa shiga kuma duk wadda kika ga dama kiyi zaki basu labari ne a masarautar Qamar Hurriya dage rigarta tayi ta daureta daga gefe shafafen cikin ta wanda sai daukar ido yake sai kuma wata yar sarka ta gold da take like a cibinta ta fito kallon matar tayi tace kafin In fara bada labari ke ya kamata ki fara basu labari tace  munafuka  magulmaciya kuyangar mutuwar tsaye tayi tana kallon shafaffen cikin Hurriya ko kyaftawa batayi Hurriya tsoki tayi ta saki rigarta tace sakara munafuka ta barta baki sake don kam taji kunya kuyangar sosai Hurriya tayi gaba abinta tabar ta tsaye tambayar wata tayi aiko ba bata lokaci ta rakata har inda suke wanki bata da sabulu don haka ta kalli wadanda suke wanki a wurin wanda suma suke ta kallonta

Tsoki tayi ta kalli wata da take kallonta kamar zata lasheta sabulu ta gani da ruwa a gefenta don haka Hurriya ta zuba ruwa cikin bokitin dake gefen yarinyar ta dauki kayan da tasan zata sanya yau saboda idan tace zata wanke duka zai dauketa lokaci don haka kala daya da zata sanya yanzu ta sanya wandone palazzo da yar top ta duka ta fara wankewa

Hurriya tanajin ana kallonta a jikinta amman tanason ta gama wanki da takeyi saida ta gama wanke kayanta tass ta juyowa tayi ta kalli yarinyar dake mata wani irin kallo Hurriya ruwan kumfa ta diba ta watsa mata nan take ta juya tana soshe kanta Hurriya ruwan dauraya ta zuba taje ta shanya kayanta inda taga ana shanya ta ajiye mata bokitin yarinyar tace mata ki kawo sauran kayan ki in wanke maki naga ke bakuwace Hurriya banza tayi da ita ta jawo wayarta ta sanya waka ta samu wuri ta zauna tana bin wakar tanajin idanu sosai akanta amman ko a jikinta kallon kafarta tayi har dan kumburi tayi ita ba ma'abociya sanya safa bace amman ya zatayi tsaki tayi

Alamun bushewar kayanta da ta ganin ya sanya ta dauki abunta ta tafi. wanka take Bukatar yi don jikinta duk ya dameta tanayin wanka fin sau biyu a rana jikinta har yanzu bai saki ba don tanajin radadi har yanzu a fatarta a waje ta hadu da Habiba

Amman bata ganeta ba Hurriya sarai taganeta zuwa tayi inda Habibar take tace ki samo man ruwan zafi inyi wanka kallonta Habiba kawai takeyi Hurriya shiru tayi tana mamakin yan masarautar basu da aikin yi ne sai kallon mutane tsoki tayi wanda ya sanya Habiba cewa to bari in samo maki a kitchen mi zakiyi dashi? Shiru Hurriya tayi tana kallon Habiba tanason karantar ta saida tagama kare mata

kallo sannan tace Bath shiru Habiba tayi alamar bata gane ba tace mata wanka da sauri habiba tabar wurin da niyyar nemo ma Hurriya Ruwan wanka bata wani bata lokaci ba sai gata da ruwan zafi lokacin har tana wurin Hurriya ta cire safarta habiba na dawowa ta mika mata kayan data wanke da safar alamar ta rike mata jiki na rawa habiba ta amsa sannan Hurriya ta shiga inda take tunanin toilet ne da kyar Hurriya take wanka a wurin saboda shegiyar kazantar dake ciki bata wani jima ba don watsa ruwan tayi ko sabulu babu ta maida kayan jikinta ta fito

A inda tabar Habiba ta amshi kayanta sannan ta shiga katon dakin har inda suka kwana itada Bintu kallon katifar tayi taga an gyara tsaff tsaki tayi jin rashin brush din da batayi ba a hankali ta dauki madubi ta bude bakinta tana kallon hakoranta da suke farare jere yan kanana kallon abinda yake gefe da gefen hakoranta tayi golden wanda sai salki yake kurama abun ido tayi tana kallo sai kuma ta rufe bakinta tare da yin tsoki abubuwa da yawa sun dameta ba abinda tazo dashi na yau da kullum na rayuwa da ace bata siye kayan nanba da batasan yazatayi ba tunawa tayi da sauran kudinta aiko ta bude ledar kallon kayan tayi don tana gani tasan anyi mata bincike bata wani damu ba itadai damuwar ta kawai sarkokinta wadanda suke taimaka mata wurin cigaba da rayuwa a hankali tajawosu taga sai sparkling sukeyi zame rigarta tayi ta kalli tatoo din dake zane a jikinta sannan ta kalli zanen sarkar da akayi design da irin tattoo din jikinta a gefe, sai Stone din dake tsakiyar sarkar dake rubuce da H baro baro kallon dayar sarkar tayi zuciyarta na kuna so take tayi kuka amman tasan ba lallai ta iya kukan ba wani wando ta zaro yana da aljihu can kasa kuma daga ciki sannan ta sanya abinta tare da addu'ar kada a dauke mata kara kallon tatoo dinta tayi wanda yake a gefen bayanta jin motsi mutum ya sanya tayi saurin sakin rigar tareda sauke ajiyar zuciya habiba kallonta tayi tana kallon rabin jikinta da ya fito saboda rigar daman buttones gareta to da ta bude rigar kusan har cleavage dinta ana gani kuma bata maida buttons din ba lumshe ido Hurriya tayi Habiba kam tsaye tayi tana kallon jikinta wanda bata taba ganin fata mai sheki da kyalli irin tata ba tana tunanin ko twins albarka.

Hurriya tanajin idonta a jikinta saidai batada energy na magana don duniyar tunanin takeson fadawa abinda ta tsana kenan rayuwarta don tunanin rayuwarta ta baya pure darkness ne wanda bata fatar wani ya tsinci Kanshi a ciki ,ta iya shutting kuma ta iya controlling emotions dinta abinda tasani shine idan har kaine kake da kanka to zaka iya controlling abubuwa da yawa saidai akwai abinda baka iya controlling saboda we're human beings kuma Humans are weak.

Please comment share and like

Love you all

[12/02, 4:53 PM] Khadyn Sp: 🌚Masarautar Qamar

By Khadija (KMU)

Page 15&16

Bude idanunta masu kyau tayi sannan ta sauke su à habiba da take binta da wani irin lustful look Hurriya zuba mata idonta masu kaifi da kwarjini tayi da sauri Habiba ta gyara tsayuwarta sannan tace kina bukatar wani Abu a hankali Hurriya tace comb da sauri Habiba ta kawo mata comb kallon dogon gashinta takeyi wanda kwata kwata bai kama dana yan Nigeria shiryawa tayi cikin wani brown palazzo sai red riga gashinta sakwa sakwa ta daureshi Habiba na kallonta kamar zata cinye ta so take ta taba gashin taji idan nata ne Amman tsoro ya hanata takalminta ta sanya ta fita batasan inda wurin yake ba saida ta tambayi wani ya nuna mata hanyar da zata bi duk inda ta wuce kallonta akeyi tanaji a jikinta kuma tasan ana kallonta saidai ta saba ko a garinsu haka akeyi mata irin wannan kallon tafiyar ma taki karewa saboda nisan tafiyar wurin.

Uban bayi ya kirga su Amman ba mutum daya acikin mata kuma ance masu su talatin ne mamaki sosai ya kamashi don haka ya nufi inda twins suke Allah ya taimaki shawata Allah ya kara maki nasara Babu mutum Daya a cikin mata kuma su talatin ne liya da mamaki take kallonshi don ba'a taba samun irin haka ba kallon neela tayi saidai hankalin Neela kwata kwata bai tare da ita yana wani saiti daban don haka ba tare da bata lokaci ba ta kalli saitin da Neela take kallo inda Hurriya take tafiya kamar she own half of the world yadda tafiyarta take cike da izza liya da mamaki take kallon Hurriya kowa a wurin hankalin shi ya koma kanta fuskar ta fayau babu komai amman wani irin tsantsan kyau da annuri ne take fiddawa gashin kanta wanda bata daure ba duk ya zubo mata kowa bude baki yayi yana kallonta da mamaki don karime kasa shiru tayi tace uwale kamar Hurriya nike gani daga mata kai uwale tayi tace itace fa karime sanya hannunta tayi a baki tana cizon yatsa

Hurriya ba inda ta tsaya sai a saitin Bintu banda faduwar gaba ba abinda bintu keji .

Cikin natsuwa ta Cire kayan jikinta  kallon inner wears din da ta siya dazu dasu sabulun wanka da brush tayi har da turare mai sanyi kamshi batasan ana kasa haja ba sai dazu da safe inda har tazo wucewa taga haule reza ta kasa kaya masu kyau har ta wuce ta dawo haule reza ba abinda bata saidawa saida Hurriya ta bata kudi sosai wurin siyen abinda takeso don saida ta tabbatar duk abinda take bukata ta siya sannan ta nufi bangaren Imad

under wears ta sanya masu kyau sannan ta shirya cikin wata blue half gown da iyakarta gwiwar kafarta ta tsaya

doguwar hijab dinta ta sanya sannan ta kabbara sallah rama sallolinta tayi duka bayan tagama sallarh ta kishingida jikin katifar ta lumshe idonta ba bacci take ba Amman dai tayi lamo

Sunanta taji ana kira saidai ko motsawa batayi ba bare tayi tunanin bude idonta saida tayi mintuna Sosai kafin ta bude idonta ta zuba ma zubaida su da take tsaye wanda tagama kulewa don tunda tazo tasan ba bacci take ba Amman don bakin rainin wayau ace tanajinta tayi shiru ta kyaleta

Zubaida ta kalleta tace Lallai ma Hurriya shine zaki zo ki kwanta wakike tunanin kinbar ma aiki sai ki taso tunda ba bayi kika ajiye ba

Don ana bukatar ki a Aikin dare shiru Hurriya tayi batace kala ba don yaddda tayi kamar ma da dutse ake maganar

Hurriya magana fa nike inji zubaida shiru Hurriya tayi saita lumshe idonta

Zubaida kam iya jin haushi takai don cikin zuciyarta banda la'anar Hurriya ba abinda take saidai tayi mata wani irin mugun kwarjinin da bata iya maida mata magana

Gajiya tayi da tsayuwa zubaida taja tsoki tayi tafiyar ta

Hurriya kam shiru tayi don saida tayi kusan minti talatin kwance idonta kuma rufe kamar mai bacci

Tashi tayi ahankali cikin yanayin natsuwarta ta sanya takalminta ta fita

A hankali take tafiya wadda idan ka kalli yadda take tafiyar zaka dauka jinin sarauta ce dogayen kafafunta da suke bude sai salki suke sai tulin bakin sumarta wadda baka iya ganin jelar gashin saidai

kwantaccen gashinta wanda ya fara tundaga goshinta farin wata ya haskata wanda ya taimaka wurin fito mata da tsantsar kyau na hallita duk wanda ya kalleta ya kara kallonta yasan mai kyau ce wato mai asalin kyau

Kallonta ake gabas da yamma kudu da arewa duk da kasancewar darene

Daidai saitin su barira da suke zaune a tabarma suna shan rake tazo zata wuce tanajin duka idanunsu dake yawo a kanta Amman ko a kwalar rigarta ta cigaba da tafiya tayi abunta

Muryar Hansa'u ce ta doki kunnenta wadda take cewa barira gafa mutuniyar

Barira shiru tayi tana kallon bayan Hurriya da dogayen kafafunta lashe baki tayi ta gyara zamanta batace komai ba

Wasila ce tace har yanzu bamu dauki fansar abinda tayi maki barira ba Amman na rantse bataci banza ba

Don ko yadda ta bata mana suna sai mun gyara mata zama sai na wulakanta yar matsiyaciyar can wulakanci mai muni sai kuma na hada mata tuggun da bazata iya warwareshi ba duka rayuwarta a masarautar nan sai na wulakantata wulakanci mafi wulakanci sannan in kaskantata kaskanci mafi kaskanci

Sannan tazo har gadon baccinki barira sai yadda kikayi da ita

Dukansu dariya suka sheke da ita tare dayin na'am da alkawarin da tayi kuma Dukansu sunce zasu tayata

Hurriya duk tanajin abinda suke cewa duk da kam tafiya takeyi kuma tayi masu nisa kallon sakarkaru marar sa aikinyi tayi masu ta cigaba da tafiyarta

Saida tayi tafiya mai nisan gaske kafin ta kawo chamber Imad

Ahankali ta shiga kitchen din wanda tana shiga kamar hadin baki duka ma'ikatan da suke aiki a kitchen din suka jiyo suka kalleta acikin su ba wanda bai bude baki ba yana kallonta ba tunda daga sama har kasa

Amman Hurriya shin ita ko ajikinta don idanun mutane basu daureta kwata kwata ko alama itadai Allah ya bata wani irin confindence wanda ba ko wani dan mutum yake da irinshi ba

Hurriya bata fasa tafiya ba don tsakiyar kitchen din tazo sannan sai taga tukunyar da ake shredded beef din don haka cikin natsuwa taje ta fara motsa tukunyar

Zubaida ce wadda ta kasa yin shiru cike da rashin kunya da wulakanci tace wai casu zaki ko coci Hurriya dagowa tayi ta zubama zubaida idonta masu kama da zaiba sannan ta tsotsi bakinta a hankali tace casu zamuje nida tsohuwarki da tsohonki idan mugama sheke aya sai mu tsaya ta coci muyi ibada

Tayi maganar hankali kwance tana kallon kowa acikinsu wanda fuskarsu take dauke da mamaki

Dukansu ba wanda bai saka wani abu acikin ranshi ba

Wasu kuma cewa suke daman tana magana?

Hurriya bayan ta tabbatar da shredded beef din yayi ta juyeshi a cikin food flask sannan ta dauki tukunya ba abinda ba'a nuna mata ba a bayani don haka tasan inda komai yake

Ruwa ta zuba a tukunya sannan ta shiga store ta debo basmati ta kunna gas ta daura tukunya hadaddiyar biryani tayi masu don tana abincin tana rera waka nike gani tanayi tana dan juya kugunta har ta gama don kamar abincin na tura mata memories don tana enjoying

Tazo ta kwaba pancake dinta ta soyashi mini sannan ta dauko chocolaté tayi dizzling dashi

Tana aikinta tana wakarta tanajin idanunsu a kanta Amman kamar babu kowa a wurin

Saida tagama yin komai ta dauko kula ta juye don abinci bai dauki wani lokaci ba tagama saboda karfin gas din dake da ci sosai

Hadawa tayi a tray don dakanta ta jera

hada wanda mama rabi tayi da wanda tayi don abinci suna da matukar yawa  mutum ashirin zasu iyacin abinci don different varieties of food ne a wurin

Bayan tagama sai ta nufi hanyar fita mama RaBI kamar tasan niyyarta don haka tace Hurriya kune zaku tsaya har su hakimi sugama cin abinci koda suna bukatar wani abu sai ku mika masu

Bata matsa ba kuma bata dawo ba Amman ga dukkan alamu maganar ta shigeta zubaida da mama rabi da wasu kuyangu guda ukku suka fara fitar da tray din abincin  da drinks da wasu manya manya non alcoholic wines

Hurriya zuwa tayi ta dauki trays din  wanda yake cike da wasu matsiyatan plate ta shiga parlon saida ba kowa a parlon it looks like Dukansu suna parlon gaba don haka Bata wani Bata lokacin ba ta shiga ba excuse ba sallama kallon mutanen dake zaune a tsakiyar parlon tayi duk twins ne kusan set uku masu matukar kama da juna.

Liya wadda ta daura kafafunta saman jikin Neela in an annoying way itace ta fara lura da Hurriya kallonta take from head to toe shiru tayi batace komai ba duka sauran hankalin su yana akan abinda sukeyi Neela hankalinta duka yana Akan wayarta sai Amrah da imran da suke playing ps 5game duka hankalisu yana a wurin game din

Liya kam satar kallon Hurriya kawai take wadda take jera abinda ta shigo dasu a dining kutt The girl is unparalleled beauty su zubaida duk sun dukar da kansu da kuyangin da suka shigo tare

Kallon kafafunta wanda suke bude tayi tana kallon sumarta da take bude fuskar nan a hade take kamar an aiko mata da sakon mutuwa tanayi tana cije lebe wanda ga dukkan alamu sorarta ce Liya kasa janye idonta tayi daga kallon Hurriya don tunda take masarautar Qamar bata taba ganin halitta mai kyaun Hurriya ba saidai gabanta ne yayi mugun faduwa tunawa da tayi ana jita jitar cewar masu kyaun masarautar su mutuwa sukeyi don ko a ma'aikata indai matane to ba'a cika kawo marar sa kyaun hallita ba saidai tunda take bata taba ganin Mai kyaun da ta kama kafar Hurriya ba wane subira an dade acikin masarautar Qamar ana bama subira sarauniyar kyau Amman wannan yarinyar tayi ma subira fintinkau don indai za'a hada kyaun subira da Hurriya to subira zata iya samun 30percent ita kuma Hurriya 70percent

Babu abinda Allah ya rageta dashi don ita jikinta irin na models ne wanda turawa suke iya barnar da ko nawa ne garesu saboda su mallaki irin jikinta

Sauke ajiyar zuciya tayi farar daya tausayin yarinyar yana kamata don tana da kyaun da ba kowani namiji bane zai iya dauke ido akanta ba sai kuma babban kalubalen dake masarautar duk da jita jita ne Amman ta dade tana tunanin anya abun ba gaskiya bane don itama ta rasa ma'aikantata Sosai wanda suka shaku kuma ta saba dasu saidai duk idan hakan ta faru akwai abinda jakadiya take fada mata saidai tun tana yadda har tazo tana putting Question mark.

Imad ne ya shigo kallonsu yayi Dukansu sannan yace guys let's eat dinner ku tafi kubar min part dina don duk kun cikamin part dina Ammar ne ya ajiye wayarshi wadda take hannunshi sannan yazo Daidai inda Imad yake ya dafa shi yace ya akayi ka kosa MU tafi kodai kodai sannan ya fashe da dariya Imad daure fuska yayi dagajin maganar Hurriya don yarinya ta bata mashi rai kuma ta rainashi shida ma'aikatan masarautar Qamar ke shakkar shi Amman yarinya yar Qarama tana Neman rainashi har sanyawa fa yayi a kira mashi ita kuma dagagan ya shanyata so yayi sai tayi awa goma tana jiranshi amman tayi tafiyarta idonshi idon Hurriya Amman sai yayi mata wukanci

Dariya ammar ya cigaba dayi yace kodai har ka folla ne? Naga yarinya is beautiful ya ida da maganar da wata irin dariya

Neela itama dariya tayi tazo saitin ammar tace who's the girl dan dungurinta ammar yayi sannan yace magulmaciya yace ban fadi sannan yayi mata gwalo

Dariya Liya tayi sannan tazo saitin ammar itama tace who's the girl bro please tell me kasan ba ajin kanmu dariya yayi sannan itama ya dungureta yace magulmata bazan fada ba

Dukansu tare suka jero sai yan kananun kannansu wadanda suke uwa daya uba daya masu bala'en kyau Amrah da hamdan kenan miskilai ne na karshe kuma yaran da basuyi ma kowa magana don duk da irin tsantsar kauna da take zagaye dasu wurin yayyayensu wadanda suke jinsu kamar kwai to idan ba yayyensu ba wanda sukeyi ma magana sun shaku da yayyansu Sosai saidai sarauta ajinisu take don wata sa'in miskilancin su harga yayyansu don tunda sukazo dinner a chamber imad wadda ta kasance duk sati sukeyinta saboda kowa yanada sashen shi to suna dadewa basu hadu ba sai Ammar ya kawo shawarar every Friday night suyi arranging cin abincin dare tare tohm haka sukeyi dukk satin duniya sai kuka suji damuwar junansu

Tare suka iso katon dining din wanda yake cike da abinci kala kala zubaida kansu a kasa suka farayi masu kirari Allah ya taimake ku Allah ya kara maku nasara sunata yi masu kirari

Duk acikinsu ba wanda ya amsa masu don ko kallon inda su zubaida suke basuyi ba

zama dukansu sukayi ta Liya ce ta juyo tace masu we will serve ourself

Hurriya tana tsaye tana kallonsu ita ba wanda tayi ma magana Liya dai na kula da ita su Imad hankalisu ma bai kai kan ma'aikatan ba bare suga Hurriya don su ma'aikatansu ko kallo basu ishesu ba.

Hurriya tsaye tayi tana kallon kowane acikinsu ba tare da ta dukar da kanta ba

Hamdan ne ya dago idanunshi daga kan iPad din dake rike a hannunshi cikin sa'a kam ya saukesu akan Hurriya da take tsaye fuskarta babu annuri kallonta yake Ko kyaftawa bayayi itama kallonshi take cikin idanu

Neela ce ta kalli Amrah tace ki ajiye iPad dinan muci abinci turo baki Amrah tayi sannan ta ajiye iPad din muryar hamdan ce ta doki dining din dasuke yace you alamar yana kiran wata Dukansu yayyanshi dagowa sukayi suna kallon wadda yake kira kasancewar shi ba mai yawan magana ba don sukansu hardly ne su ji maganar shi saboda miskilancin shi

Hurriya da take tsaye tasan da ita yake kallonta yayi sannan ya kara nunata da yatsa still banza tayi ta kyaleshi tana zuba mashi idanunta

Imad wanda shima hankalin shi nakan wayarshi ya dago ya kalleta saida ya kalleta tundaga farko har karshenta aranshi yace Lallai ma yarinyar nan waye zata burge tazo masu a haka kamar zata club saidai bai iya yaudarer zuciyar shi ba Amman yarinyar gaskiya tana da kyau toh kila shiyasa take raina ma mutane wayau amman bari zaiyi maganinta aiko nan take ya bata rai ya hade fuska yana kallonta

Ammar wanda shima kallonta yake bai ko kyaftawa saida ya tabbatar ya saisaita kanshi sannan ya kalli Imad da yake ta cin magani ya kwashe da dariya

Hamdan ahankali ya karayi mata magana yace please come and join us banza ta karayi dashi

Imad ne ya tashi ranshi bace Ammar yayi saurin rikeshi yana dannah dariyar shi

Amrah ce ta taso tazo saitin Huriya cikin muryarta ta yarinta tace kizo muci abinci tare don Allah tana pleading dinta da hannu in a cute way Hurriya kallon yarinyar tayi mai bala'en kyau amman kallo daya zakayi mata kasan akwai kadaici tattare da ita shiru Hurriya tayi tana kallon hamdan da amrah wanda shima ita yake kallo da alamar tazo tayi joining dinsu Neela ce ta kallesu ta bata fuska sannan tace what are you doing Amrah

Amrah bata fuska tayi haka zalika hamdan Liya ce ta taso tazo saitin Hurriya sannan tace please join the poor babys they love you

Hurriya daga mata kawai tayi ta zauna family dinner din

Zubaida kam kamar ta mutu saboda bakin ciki yarannan da basu tabayi mata magana ba don yaran Allah ya zuba masu mulki da sarauta basu kula kowa gashi yayyansu kamar su cinyesu haka sukejin su aransu idan sun soka tohm tohm yayyen sun soka idan sunki ka tohm suma sunki ka

Hamdan ne ya kalleta cikin mulki da sarauta don kusa da kujerar da yake tazauna ahankali yace mata you're beautiful shiru wurin ya dauka kowa yana saka Abu aranshi Imad kam zuciyarshi banda bugawa ba abinda takeyi saboda tsanin bacin rai

Imad magana zaiyi Amrah ta rigashi ta hanyar dawowa saitin Hurriya tace ya sunanki please?hurriya kallonta tayi da idanunta masu kwarjini Amrah dafe zuciyar ta tayi ta hanyar cewa please stop looking at me like that way,you look intimidated .i know you're more beautiful when you smile ok can you smile for me just once tana mata wink

Hamdan dariya yayi wadda ta fito tundaga zuciyar shi sakin baki su Ammar sukayi suna kallon kannansu

yare Hamdan yayi ma Hurriya ta hanyar cewa zaki bani diyarki idan kika haihu you're beautiful but you're lonely ta ko ina

gaban Hurriya ne ya shiga faduwa tana kallon hamdan da ya tsare ta da idanunshi yana jiran amsarta

Rabon da taji kalar yarenan har ta manta innallilahi wa'ina ilahi raji'un ta shiga furtawa cikin zuciyarta wadda take duka kamar ganga rabon da ta ambaci sunan Allah rayuwarta ta manta saidai acikin Sallah wadda batada tabbacin tana amsuwa ko bata amsuwa

Hamdan ya saki wani killer smile wanda idan ka kalleshi zaka iya cewa babba ne wanda dudu shekararshi sha biyu a duniya shida twin sister shi

Saidai Allah yayi mashi baiwa wadda ake kira wato smartness

Shiru duka wurin ya dauko suna kallon Hurriya da Hamdan murmushi Hamdan yayi yace mata you look like princess Layla Al-Khasheem she's my role model because speech dinta yana matukar taimakona did you know her ?dan murmushi yayi sannan yace i know you will not know her saboda celebrity ce a duniya baki daya duk wanda ya kalli Hurriya alokacin zaisan a tsoroce take don sam takasa boye firgicin dake fuskarta salati take Sosai acikin ranta

Amrah ce tace she really look like Layla Al- khasheem sai yanzu da ka fada na lura

Ammar ne ya kalli Hurriya yace sunyi kama Sosai ya sakar mata murmushi tare da cewa you look like Layla Khasheem daga yadda yayi maganar zakasan cewar Dukansu suna kaunarta don liya itama washe baki tayi

Hurriya kam duk ranta ya jagule don kamar tana zaune saman kaya ko garwashin wuta haka takeji tsoro da fargaba suna kara cikata

tanajin saukar idanunwan kowa akanta

Amrah ce tazo saitin Hurriya tareda dafa mata kafada tace mata can you be my friend da wani irin karfi Hurriya ta ture ta ta fadi kasa fuskarta na nuna zallar bacin rai tace wa ya baki damar taba ni tana binta da idanun masu nuna zallar bacin rai saidai tana kokarin saita kanta saboda batasan yanayi fuskarta ya canza saboda da wuya Hurriya ta canza yanayin fuskarta zuwa damuwa ko farin ciki ko firgice ko kuma gazawa ko gajiyawa da rayuwa fuskarta akoda yaushe a yanayi daya take wato ta daurewa  wadda za'a iya kiranta bata da mutunci

Imad ne ya tashi yazo Daidai saitin Hurriya wadda take idonta har wani jaa yake kawowa

Shima imad din rannshi a matukar bace shida neela zuwa yayi zai dauke ta da mari Ammar yayi saurin rikeshi Imad please don't touch her ba tarbiyya bane dukan mace.

Hurriya Dukansu kallonsu tayi ba tare da tace masu komai ba ta fita daga dakin Hamdan ne ya ruga zaibita Liya ta rikeshi

Amrah kam kuka takeyi sosai wanda yasanya duka hankalin su ya dawo kanta

Neela ta rungumota tana lallashinta Ammar shima lallashin yakeyi Imad tashi yayi ya shige daki zuciyarshi na tafarfasa sannan ya barsu a parlon

Hurriya har bata ganin gabanta da kyar take tafiya ga dare da yayi ga sanyi ga fargaba abubuwa duk sun hade mata

Da kyar ta kawo kanta dakinsu tsitt kakejin ko ina adakin wani irin shiru wurin ya dauka don da yawansu sunyi bacci .

Ahankali ta kwanta tare da lumshe idonta tana fadawa duniyar tunani tambayoyi take ma kanta ina wannan yaron ya iya yaren Amarich sannan yace suna kama da Princess Layla Al-Khasheem shin har yanzu kamarsu a bayyane take itada Layla

Zuciyar tace ta buga don tana tsoron kalubalen da zata iya fuskanta nan gaba idan har identity dinta ya fito fargaba tsoro kadaici duk sune suka suka cikata

Bacci ne ya fara fizgarta Mai cike da gajiya ahankali baccin ya fara nauyi saidai saukar Ruwa mai matukar sanyi ajikinta ne ya sanya ta farkawa da sauri kuma a firgice bata Ida warwarewa ba taji an kara zuba mata ruwan mai matukar sanyi ga yanayin sanyi irin na farkon January

Rungume jikinta tayi idanun ta da hakoranta na gab gab wani ruwan taji ankara zuba mata mai matukar sanyi numfashinta ne ya fara ja yana dawowa kirjinta yana wani irin duka gab gab kankame jikinta ta karayi numfashinta na rage sauri dariya suke a kunnenta suna ihu suna kashewa

Tafiya su barira sukayi suka barta tana kokarin saisaita numfashin ta saidai mi ba abinda take gani irin past dinta rayuwarta ta tabaya yadda kawunta yake zuba mata ruwan kankara  yana dukanta ne ya dawo mata kanta ne ya farayi mata wani irin nauyi sai wani irin duhu da ta fara gani sannan numfashinta ya dauke.

Hello readers ya kuke tunanin  salon labarin namu

Ya akayi Hamdan yayi wani yare wanda Hurriya kadai takejin yaren

Miye tsakanin Layla Al -Khasheem da Hurriya Faisait Hamood

Ga Amrah da Hamdan da suke tsanin son Hurriya mi yasa suke sonta?

Ga Barira da suke barazanar tsoma kansu a rayuwar Hurriya anya basu debo ruwan dafa kansu ba

Ga wasba yar yarinya Karama da Hurriya ke burgeta

Miye yake faruwa ne da kyauwawan masarautar Qamar wanda ya sanya ake kiran masarautar da mysterious palace

Wacece Hurriya?

Ku biyoni cikin labarin masarautar Qamar a hankali komai zai warware.

Waye star dinmu a maza?

Shaho,Kumurci,imad ko Ammar kuma Hamdan

Muje zuwa kawai don salon labarin namu ya bambamta da kowani irin labari.

[12/02, 4:53 PM] Khadyn Sp: 🌚Masarautar Qamar

A story about a mysterious palace

By Khadija (KMU)

23&24

Kwance take male male cikin ruwa mai matukar sanyi wanda kwata kwata bata ko numfashi ba wanda ya lura bare ya ankara

Da kyar suka lallashi amrah aka sanya kuyangu suka tafi da ita chamber dinta Mai matukar kyau da daukar ido

ruwan wanka Neela tazo ta hada mata ta fito mata da kayan bacci sannan tayi mata addu'a tare da kashe mata wuta

Liya kam tare suka tafi itada Hamdan don ba wanda yace ma dan uwanshi komai har suka isa chamber dinshi

Ammar shima chamber dinshi ya nufa ya haye saman gado tare da lumshe ido yana tunanin duka abinda ya faru yau so yake ya hada komai wuri daya don samun ma'anar abun saidai ya kasa hada komai

Amman yarinyar tayi matukar bata mashi rai donmi zata ture Amrah shiru yayi yana tunanin kilan tana da uziri don kowa da uzirinshi.

Karfe 5:44 Allah ya kawo Bintu domin tada Hurriya sallah asuba saidai ganinta kwance ya sanya ta fasa ihu agigice tazo tarinka tadata tana Hurriya Hurriya ki tashi don Allah ki tashi ki daina bani tsoro inna lillah wa'inna ilaihi raji'un Bintu ta shiga furtawa tana bude ma Hurriya ido Amman shiru

Ruwa ta debo da sauri ta yayyafa mata tare da shafa mata a fuskarta bude idonta Hurriya tayi wanda sukayi matukar jaa wani seizure numfashin ta ya fara tana tari mai sarkewa don kamar zata mutu haka numfashin yakeyi ga kuma tarin yaki sassauta mata Bintu banda hawaye babu abinda yake kwarara daga idonta don ta rasa mi zatayi wanda zai taimaka ma Hurriya saidai kukan

Kirjin Hurriya taga yana sama yana kasa numfashinta yazama abnormal don abinda take yafi nada bintu sakinta tayi ta ruga ta fita aguje ta rasa ma inda zataje watar yar matashiyar budurwa tagani tace mata don Allah akwai likita anan yar budurwa tace Akwai inna hanne mai bada taimakon gargajiya idan ansamu mararsa lafiya godiya kawai tayi mata batasan ya akayi ba sai ganin ta tayi a kitchen. ganin kanta a kitchen datayi ya sanya ta fashe da wani irin kuka inna hanne ce ta kalleta tace ke kuma lafiya kike mana sintiri kina kuka

Bintu zuwa tayi ta rike mata kafafunta tace ki taimaka mani ki ceci rayuwar Hurriya ta kusa mutuwa ki taimkeni yatsine fuska hanne tayi sannan tace wacece kuma haka Hurriya yar doguwa mai kyau tureta hanne tayi tace ni likita ce da zaki zo ki tsareni da magiya

Ki taimake ni don Allah ko nawane nayi maki alkawarin idan ta warke zan baki shiru hanne tayi tana tunani kafin ahankali tace muje.

Barira dasu wasila ne sukaje wurin da Hurriya take yashe kwance Hansa'u ce ta ture mata dogayen kafafunta ahankali Hurriya ta bude idonta wanda suke rufe hakoranta suna gab gab kirjinta na sama na kasa binsu take kawai da kallo dariya suwaiba tazo tayi tana take mata yatsun hannunta ita kuma barira ta take dayan hannun da nuna itadin watace tayi dariya tace yau zan kwanta da wannan kaskantaciyar baiwar sannan na sanya a farfasa mata jikinta sai inbi tada gishiri a ko ina kuma kullum kowa da kowa acikinku zai kwanta da ita sannan zansa bawa mafi muni da kaskanci ya kwanta da ita ta fasa wata dariya  su Hansa'u suma sukayi dariya Hansa'u ce ta kalli barira sannan tace ina fatar a aske mani gashi kanta murmushi barira tayi sannan tace angama

Wasila ce ta fashe da dariya tazo ta haye Hurriya tare da kama hannun rigarta zata farka mata riga

Hurriya kam ta kanta takeyi don numfashinta kiris ya rage ya kara daukewa Amman tana cikin tsananin tsoro don tabbas idan har ta bude mata baya dolene taga zanen tatoo din dake da tambarin daga inda ta fito nobody is allowed to see the tatoo idan ba haka ba rayuwarta will be at more risk don tatoo din shine yake rike da sirrin ko ita wacece miye zai faru da ita idan wani yaga sirrin dake Zane abayanta

Shiru tayi zuciyarta da kirjinta na wani irin bugawa hannun rigar aka farke wanda hakan ya kasance daidai da daukewar numfashinta.

Bintu da inna hanne da suka shigo yanzu wanda yayi Daidai da daukewar numfashin Hurriya da kuma ida farkewar hannun rigarta

Wani irin kyakyawan mari inna hanne ta dauke wasila dashi tana binsu da wani irin matsiyacin kallo rike kuncinta wasila tayi ta fita daga wurin a hankali Hansa'u ta bita a baya sauran ma Dukansu suka bita a baya duk a masarautar nan ba wanda Suke tsoro irin inna hanne da reza dan daya hatsabibiyace daya kuma fitinaniya ga uban karfi

Bintu kam rungume  Hurriya tayi tana kuka inna hanne ta kalleta tace ta fita ta debo masu ruwan zafi Bintu ta tafi don samo ruwan zafin

Taba Hurriya inna hanne tayi saidai abinda tagani saida ya girgiza ta daman har yanzu tanada aljanun da suka so bude mata ido kenan to mi ya kawosu miyasa suka karantar da ita bayanin Hurriya abinda rabon da tasan wani abu game da rayuwar wani andade

Inna hanne kallon Hurriya take tana tunanin abinda tagani tattare da rayuwar yarinyar lallai Hurriya tana cikin hadari acikin masarautar nan don irin duhun da tagani da kalubalen dake lullube da ita sunan Allah kawai inna hanne take fada don ta dade bata ga Abu irin haka ba

Don kwata kwata aljanun da suke son bude mata ido sun tafi tare da karfin ikon Addu'a da azkar don bata ganin komai tafi shekara goma rabonta da budewar idon jinnu sai wannan karon mi hakan yake nufi Akwai matsala babbar matsala tattare da rayuwar yarinyar nan

A hankali ta daga rigar Hurriya a firgice tace masarautar Heral Inna lillah wa'ina ilahi raji'un ta ambata tana kallon zanen tatoo din Hurriya dake kwance agadon kafadarta ta baya kenan itace yarinyar da kusan shekara biyar dasu ka wuce akazo ana nema don kusan ko wace babbar masarautar dake duniya anje don harda masarautar Qamar akazo tare da alkawarin duk wanda ya samota akwai gagarumar kyautar da za'ayi mashi don dashi da zuri'ar shi hatta tattaba kunnenshi sun gama talauci saboda irin zunzurutun abinda aka alkawarta sannan kuma idan nameji ne zai aureta tare da nadashi sarautar kasar baki daya

Shiru tayi tana hasko Labarin irin masarautar Heral da ake basu irin mulkin da akeyi da irin tarin arziki da daular dake shimfide a cikin kasar don masarautar na daya daga cikin jerin masarautar duniya da ake ji dasu

Shiru tayi tana tunanin duhun da tagani tattare da Hurriya wanda ba'a masarautar Qamar kadai ya kare ba hatta masarautar Heral din idan ta koma zata fuskanci kalubalen da kilan zai iya sanadin rayuwarta don ko masarautar Qamar din Qalubalene da zai iya sanadin rayuwarta ko kuma ya tarwatsa mata duk wani farin ciki na rayuwarta wanda yarinyar ga dukkan alama ta dade ba farin ciki rayuwarta

Inna hanne ta sauke ajiyar zuciya tana kallon kyakyawar fuskarta tana nazarin dalilin da aljanunta sukayi nuna mata bayanin Hurriya yarinyar abar tausayi ce saboda zagaye take da makiya  Amman In Sha Allah zata taimaketa da addu'oi Sosai da azkar masu matukar muhimmanci saboda tasan tsafin da akeyi a masarautar Qamar

Bintu ce ta shigo aguje da ruwan zafi sannan ta ruga aiken da inna hanne tayi mata don amso mata magungunan hausa Bintu bata wani dauki lokaci ba sai gata da magungunan

Kallon Bintu baba hanne tayi tace ta dan fita Bintu batayi musu ba ta basu wuri

Maganin ta hada mata na lamoniya hade da sanyi sannan ta bude bakinta ahankali ta shiga bata don ko motsi batayi rabin maganin na shiga rabi na fita baba hanne kallonta take cike da tausayinta don itadai tunda ta taso rayuwarta A daji kuma babansu magani yake badawa itama har ta gaje shi to bata taba cin karo da makamanciyar lamoniya irin wannan ba

Bayan tagama bata magani ta samu farin tsumma mai kyau sannan ta shiga gasa Hurriya da ruwan zafin

Tana dora hannnunta ajikin Hurriya ta zabura

Haka ta rinkayi da ta taba mata jiki sai ta zabura saida ta taimaka mata sosai wurin ganin gasa jikinta da magungunan gargajiya

Wasba ce zaune à inda Hurriya tazauna jiya tayi wanki tana wasa da karamin icce wanda ke nuni da kamar Hurriya take jira

Kallon hanyar da ta biyo jiya tayi saidai bata ga ko mai kama da ita ba

Bata rai tayi tana turo baki ta tashi ta koma cikin gidansu

Hurriya shiru shiru bata tashi ba saaidai Bintu na zagaye da ita kamar wacce zata gudu don har tayo aikinta ta dawo

Inna hanne ta dade a wurin tana kula da ita kafin ta koma kitchen domin ayyukanta  saida Inna hanne tagama ayyukanta sannan ta dawo inda Hurriya take kwance hannunta rike da kofin shayi cikin hikima ta shiga zuba ma Hurriya ruwan shayin duk da rabi ya shiga rabi ya fito haka abun yake

Bayan tagama bata shayin tayi tagumi tana tunanin ikon Allah tunda take bata taba tunanin ko a rayuwarta zata iya zuwa masarautar Heral ba saboda sai an ketare kasashe shin bama wannan ba itadin wacece ba kowa bace face ma'aikaciya a masarautar Qamar sai kuma Qaddara da ta hadata da long lost princess din Qasar

Saidai Tana Addu'a Allah yabata ikon taimokon yar marainiyar yarinyar nan Allah kada ya sanya san zuciya ya debeta ta tona mata asiri

Su kuma su barira zatayi maganinsu Lallai da ace sun san wacece ita da ko hanya daya basu isa su hada ba

Don duk yan masarautar Qamar tafi karfinsu hatta sarkin idan tagadama tace a sauke shi daga kan mulki to tabbas babu tantama za'a sauke shi don masarautar su tana mulkin masarautoci da yawa a

afirca so masarautar Qamar na ciki

Ta dade tana tunanin sannan ta tashi ta fita tana fita saiga Bintu na shigowa dan sauke ajiyar zuciya tayi sannan tace ki kula da ita don Allah.

Abun kamar wasa Amman har yanzu Hurriya bata bude idonta ba har anyi wata daya da sati daya

Su barira suna sane da halin da Hurriya take ciki don har anfara yada jita jita su barira sunyi kisan kai saidai da yake su din suna da power sosai ba wanda ya tarbesu da maganar

Saukin Hurriya daya data samu Inna hanne tayi bake bake ganin taji sauki don lallabata take kamar kwai kowa yana mamakin dalilin don baba hanne bata da irin wannan kirkin da take nuna ma Hurriya don itama ba Ruwanta da kowa

Bintu kam ta zuge ta rame tass kallo daya zakayi mata kasan cewar tana cikin matsinaciyar damuwa .

Imad kam shima ya shiga damuwar rashin ganin mai aikin nan don Hamdan da amrah duk sun gigita su don yanzu a chamber shi suke kwana Neela kam batasan mi zatace ba a al-amarin don tun tana kushe su yanzu ita kanta burinta da fatanta a samo Hurriya

Imad yafi kowa damuwa don kowa kallo yake yasan inda take don yanzu haka suna tare da Ammar ne a balcony Ammar ya kalleshi yace twin Imad kallonshi yayi yana daga mashi kai dafashi Ammar yayi yace nifa na rasa gane mike faruwa wacece wannan yarinyar miye hadinta da Hamdan da Amrah mi yasa suke sonta har haka yaran da basu damu da kowa ba rayuwarsu Amman sun damu da ita fiye da yadda suka damu damu

Shiru Imad yayi yana nazarin maganar saidai baisan yadda zai hada komai ya bashi ma'ana ba don haka ba tare da karayin wani tunanin ba yace Allah yasa lafiya dai

Shiru Ammar yayi sannan yace ka tambayi ma'aikatan ko lafiya? Girgiza kai yayi yace mashi Aa

Shigowar Liya ne ya sanya  Dukansu suka juya suna kallonta cikin jumpsuit din Rimowa wanda sukayi mata kyau sosai zuwa tayi gefen imad ta rike mashi hannu tace na samo labarin maid dinka ka kwantar da hankalin ka

Ammar ne ya zagayo ya rike ma Liya hannu yace lafiya miye ya faru shima rike mashi hannu tayi , murmushi tayi sannan ta gyara zama tace kwantar da hankalin ka tana cikin masarautar Qamar

A hankali ta zayyane masu duk abinda aka gaya mata ance bata lafiya har yanzu batasan inda kanta yake ba tundaga ranar da ta ture Amrah

Shiru sukayi suna kallon yadda takeyi masu bayani har takai karshe ba wanda yace kala Ammar ne yace wani irin ciwo take Liya tace bansaniba Imad baice komai ba ya tashi ya bar masu wurin ba wanda ya damu da tashin da yayi saboda susan halinshi na miskilanci

Hamdan kam ko da yagama jin bayanin da Neela da Liya suka gama mashi sai ya fara sauke ajiyar zuciya kallonshi suka rinkayi da mamaki don abinda basu taba gani bane

Amrah ce ta shigo jikinta sanye da wani crazy jeans sai yar top kunnenta sakale da AirPod Dukansu kallon yar autarsu da damuwa ta bayyana a fuskarta sukayi Hamdan ne ya tashi yaje saitin da take sannan ya zare AirPod din kallon shi tayi ta dage mashi gira guda daya alamun lafiya

Cikin muryar shi mai dadi yace I found her Amrah kallonshi take da alamar bata gane nufinshi ba murmushi yayi mata sannan yace the beautiful young lady bude hakoranta tayi tana kallon hakimi tace like seriously daga mata kai kawai yayi Amrah zuwa tayi ta rungume Hamdan tana mai tsananin murna

Inna Hanne zaune tayi tana kallon Hurriya wadda fuskarta tayi fayau gashin kanta da girarta kwance sai bakinta da yayi pink  ta riga ta gama sawa a ranta idan har Hurriya ta cike wata biyu bata samu sauki ba to zataje kauyensu ta taho da yayanta domin ya dubata

Tausayin yarinyar takeji sosai don yarinya mai gata kamarta yaushe ne Zata jira wani maganin gargajiya saidai da yanzu tana asibiti kasar waje Maganar Bintu da taji ya sanya ta dawo daga dogon tunanin da ta shiga ta kalleta sannan tace kindai ci abinci ko? Daga mata kai tayi

Wasba kije innani na kira wani karamin yaro ya gaya mata dauke kanta tayi daga kallonshi hawaye na zuba a idonta yau tasan dukan tsiya zataci bare tun dazu innani take kiranta Amman taki zuwa ta tsaya tana duba hanya ko zataga inda Hurriya zata bullo

Tashi tayi tana kuka tana share majina har tazo dan karamin gidansu dake cikin masarautar Qamar

Aiko tana shigowa innani ta rufeta da duka tana zaginta shegiya daga gidan ubanwa kike yar iska matsiyaciya tsintarciyar mage kin raina mutane ko ta cigaba da dukanta ba tausayi bare tausayawa har saida taga tana Neman daina numfashi ta daina dukanta.

Hurriya a hankali ta fara motsa yatsunta kafin ta bude idanunta Bintu dake zaune ta saki tagumi jin motsin da tayi daga Hurriya ya sanya ta kalleta cikin mamaki taga idon Hurriya bude suna kallonta da wani irin jin dadi da murna Bintu ta nufota girgiza mata kai Hurriya tayi tana mata kallon kada ki sake ki tabani

Daga mata kai Bintu tayi tana ta hamdala Hurriya kuma kallonta kawai take yadda take murna

Shiru Hurriya tayi tana tunanin wadanda suka sanyata jinya inda ace a masarautar Heral ne to babu abinda zai hana su bakunci lahira don abinda suka aikata hukuncinshi kisa ne how dare they messed with Princess wani evil smirk tayi don ita she's someone that doesn't take nonsense from anybody whether she's princess or slave tasan sai tayi maganinsu ita batajira wani ya kwatar mata yanci da kanta da hannunta zata kwatar ma kanta yanci

Hurriya bata da dadi ko kadan idan ka tabata zatayi masu salon azabar da ko a masarautar Qamar ba'a tabayi ma waninsu irinta ba because they almost killed her lamoniyar dake gareta is not an ordinary lamoniya ciwo ne mai hade da poison wanda yake babbar barazana ga rayuwarta all this while tasan Allah ke tsareta and nobody knows about her health condition don ko a masarautar Heral ciwonta is a secret duk wanda yasan da ciwonta sai yabar masarautar tare dayin nesa sosai da masarautar zatayi masu abinda idan akace gobe su kara bazasu kara ba tayi alkawarin sai sun biyata with bigger price Dukansu sai sunyi jinyar da tafi tata tayi wani evil smirk tare da rufe idonta masu kyau tana taune lebanta.

[12/02, 4:53 PM] Khadyn Sp: 🌚Masarautar Qamar

A story about a mysterious palace

By Khadija (KMU)

25&26

Bintu kallom Hurriya kawai take with pure love Hurriya lumshe ido tayi tana yamutsa fuska alamar jikinta na damunta Bintu tace bari in kira maki baba hanne ta kara dubaki

Bintu aguje taje kitchen ta kira Baba hanne wadda take tuka tuwo ai tanajin ance Hurriya ta farfado ta saki muciyar ta rugo aguje sai dakinsu Bintu murmushi tayi tana biyota a baya

A kwance suka iske Hurriya tadan tada kanta da bango ta lumshe idanunta dogayen lashes dinta kwance sai kyalli suke sai pink lips dinta da take dan cijewa Inna hanne kara kallon Hurriya tayi don ba karya tanada kyau kallonta ta karayi ganin irin kwarjini da kuma tsantsar mulki da yake bayyane ajikinta dama saidai idan baka gani Amman kallo daya zakayi ma Hurriya kasan jini sarauta ce bude idonta Hurriya tayi aiko da sauri inna Hanne ta sadda kanta kasa duk tasha jinin jikinta ta kasa motsi Hurriya kallo daya tayi mata ta kauda kanta

Hurriya Bintu ta kalla tace Bintu ki samo man ruwan zafi inyi wanka da sauri Bintu tace to inna hanne ce tace kije kitchen kice nice na aiko ki a zuba maki ruwan zafi Bintu juyawa tayi ta fita domin amso ma Hurriya ruwan wanka

Inna Hanne kam kanta duke a kasa Hurriya batasan ma Allah yayi wata hallita a wurin ba har Bintu ta kawo mata ruwan a hankali ta sauko kafarta wadda tayi mata nauyi da sanyi

Bintu har tazo zata taimaka mata girgiza mata kai Hurriya tayi alamar bataso da kyar ta iya tashi ta fara tafiya a hankali Bintu ta shiga ta ajiye mata ruwan sannan ta bata brush da macline sai sabulun wanka

Saida tayi brush sannan ta mika ma Bintu brush din ita kuma ta shiga toilet domin yin wanka

Ta dade cikin toilette tana wanke jikinta saboda kyankyamin da takeji saida tayi kamar zataji ma kanta ciwo saboda yadda take dirzar jikin sannan ta dauraye jikinta ta fito tana mai jin matukar kyankyamin kayan da ta maida

Hurriya dakinsu ta shigo inda tayi sa'a Bintu da inna hanne basu nan don inna hanne ce tacema Bintu suje kitchen tare domin dafa ma Hurriya abinci dajin haka Bintu taita murna sannan tabi inna hanne kitchen din kallon Bintu tayi sannan tace mi Hurriya tafiso acikin abinci shiru Bintu tayi sannan ta girgiza ma inna hanne kai alamar batasani ba don bata taba ganin Hurriya na cin abi da farin ciki ba don kullum cikin dacin rai take cin abinci kamar dole

Inna hanne murmushi tayi ta debo dankali wanda bai kai goma ba sannan ta fere.

Hurriya kallon ko ina tayi da yayi datti cikin yanayin natsuwarta ta amso tsintsiya wurin uwale da murna uwale ta farayi mata ya jiki daga mata kai Hurriya kawai tayi tazo ta gyara dan wurin ta share wurin tass

Sannan ta cire kayan jikinta vaseline ta shafa ta bude ledar kayanta ta zaro jeans dark blue sai farar top mai shara shara saida ta sanya inner wears hade da vest sannan ta sanya rigar

Kwanciya tayi ta mike kafafunta ta lumshe idonta tunani take neman ta farayi wanda sam babu lisaafin tunani a rayuwarta bude idonta tayi sai kam ga giftawar su barira kallonsu tayi Dukansu tana karantar su

Inna hanne ce ta shigo itada Bintu inna hanne rike da yar karamar kula mai kyau Bintu kuma hannunta rike da ruwa da plate

Da sallama suka shigo kallo daya Hurriya tayi mata tagane ta don itace matar da ta fara bata ruwan zafi. acikin zuciyar ta take tambayar kanta mi takeyi anan Shiru tayi tana kallon matar sai sadda kai take kamar munafuka tana durkusa mata alhalin ranar farko ba haka tayi mata ba

Inna hanne ta zuba mata faten dankalin da tayi mata wanda yaji kayan miya ta mika mata Hurriya kallonta tayi ba tare da ta amsa ba don haka Bintu da sauri ta amsa tazo ta mika mata amsa Hurriya tayi sannan tace Bintu ta miko mata ledar kayanta ba musu Bintu ta miko mata ledar kayanta spoon ta dauka cikin kayanta saida ta daurayeshi sannan ta faraci lumshe ido tayi ta cigaba daci wanda alama ke nuni da tana enjoying abinci

Dukansu kallonta suke inna hanne kanta a kasa saida taci Sosai sannan ta ture plate din Bintu ta kalleta sannan tace kin koshi daga ma Bintu kai Alamar Eh ta koshi

Pure water inna hanne ta miko mata alamar ta ajiye tayi mata inna hanne ta ajiye mata dauka tayi ta fasa ta shanye

Inna hanne ta miko ma Hurriya magani ba tare da tayi musu ba ta amsa tayi chokali uku ta mika mata murmushi inna hanne tayi tana mai jin dadi ganin Hurriya har tayi acknowledging dinta

Kwanciya Hurriya tayi tareda lumshe idonta tana mai neman fadawa duniyar tunani tana tuna lokacin da idan ciwon ta ya tashi yadda iyayenta ke shiga tashin hankali sosai ganin tana Neman ta fada duniyar tunanin wanda bata cika son haka ba don haka ta tashi wayarta ta dauko wadda ta dade batayi amfani da ita ba ta kunna waka sannan lumshe ido tana bin wakar fire on fire by sam smith a haka har bacci ya dauketa

Inna hanne bayan tagama aikinta ta shigo ta iske Hurriya kwance tana Bacci kamar karamar yarinya duk da bacci take amman zaka iya gane yadda ta hade fuska murmushi tayi sannan tace rigimar Duniya

Hurriya bayan ta warke saida tayi kusan sati biyu bata fara zuwa aiki ba don so take sai sanyi ya gama fita daga jikinta tasss don a lamarinta batasan weakness ko kuma ace wani ya gane weak point dinta shiyasa saida ta tabattar da ta warke tasss sannan zata koma aiki

Bangaren kam inna hanne kam hidima takeyi  mata babu kakautawa don abinci masu dadi kala kala takeyi ma Hurriya Ruwan wanka kam kullum ita take tafasa mata ta kai mata toilet hatta kayan Hurriya kwana uku sukeyi sai ta daukesu ta wanke mata

Duk hidimar da take ma Hurriya bata taba ce mata ta gode ba don kamar daman dolen ta ne ita kuma Inna hanne bata taba kallon Rashin kulawar da Hurriyyar take mata ba as wani abu ba

Tana addu'a kullum Allah ya bama Hurriya ikon yadda da ita duk da ta fahimci Hurriyar kamar bata yadda da kowa ba

A bangaren su Imad sun baza ido suna taso suga ko ta ina zata bullo don Liya ta bincika masu ance ta warke don Hamdan da Amrah kullum sai sunce zasu je Amman yan'uwan sunki barinsu saboda zai zama abun fadi a masarautar duk dasu ba ruwansu

Fitowar ta daga wanka kenan daga ita sai zani sai kuma doguwar hijab dai dai zata shiga ciki  su kuma suna fitowa Dukansu kallonta sukeyi tundaga dogayen kafafunta har zuwa kyakyawar fuskarta wadda babu fara'a saidai zallah kyau da annurin dake fita kafe su tayi da idanunta masu masifar kyau saidai baka iya jure kallonsu saboda yadda suke imnating danger flames ne kawai ke fita daga idanun acikinsu ba wacce bataji shakkarta ba saboda wani kwarjini da ta karayi masu

Saida ta kare masu kallo tass sannan ta shiga daga ciki inna hanne da Bintu na ganin dawowarta suka tashi inna hanne ta kalli Hurriya sannan tace mi zakiyi yanzu cewa tayi sallah shimfida mata dadduma tayi sannan suka fita domin bata wurin saboda shiryawa don sun san bata sanya kaya wani na kallonta

Wata doguwar riga ta sanya mai kyau saidai tana kama da abaya yau kawai taji tanason dan decent dressing dankwali ta daura ma gashinta wanda yake ta kamshin mai na soulmate don Hurriya na yawan wanke gashinta sai ta jirashi ya bushe ya gama shan iska tukuna ta shafa mai ta sharce shi.

Hijab ta sanya tayi sallah hade da rama sallahr da ake binta don daman yaune karshe idan ta rama la'asar tohm sauran magriba da isha'i

Tana gama sallahr inna hanne ta shigo wadda dama dama yanzu Hurriya na kula ta saboda tana kula da ita duk wani motives nata tana kallo duk da tana nuna halin rashin damuwa gareta ganin batada wani motives shiyasa ta kyaleta ta shigo rayuwarta kuma she knew she's too smart itadin fa sunanta Hurriya Faisait Hamood she's her fathers daughter wanda zai iya cutar da ita yanzu ai sai yayi babban shiri beside ba wanda yasan kowacece ita saidai she have to be very cautious duk dama ita din she's always cautious

Turarenta ta fesa mai saukin kudi sannan ta fito domin samun iska wayarta kirar burin yar garuwa sai a hannunta sai earpieces dake makale a kunnenta wakarta takeji wasba ce tazo inda take tana kuka tana sharbar majina kallo daya Hurriya tayi mata taganeta

wasba yar karamar yarinyar ta dukar da kanta tanata sharbar kuka Hurriya batace mata komai ba har ta gama kukanta

Saida tagama kukan sannan ta kalli Hurriya ta washe mata baki tace kinyi kyau kinfi kyau a haka Hurriya batace mata kala ba Amman tana kallon yarinyar surutai wasba ta farayi mata tace ina kikaje ne kullum sai nazo na jira inga ko zaki zo Amman baki taba zuwa ba sai yau yar dariya wasba tayi tace bari muga kwana nawa nayi banganki ba hannunta ta fara kirgawa kamar wata yar baby har saida ta kirga kwanakin da tayi bataga Hurriya ba tashi tsaye wasba tayi idonta na cika da kwalla sannan tace ki yawaita yin addu'oi Saboda banason na rasaki irin fareedaa you're beautiful ta sakar mata murmushi sannan ta ruga ta tafi

Kallon bayan yarinyar da take gudu tayi wadda damuwa ta bayyana a duka fuskar yarinyar Hurriya can kasan makoshinta tace what is wrong with the girl aranta tace ina ruwanki

Kallon mutanen da suke wucewa suna kallonta tayi itadai  tanajin wakarta tana kallon kowa da kowa

Hurriya ta dade zaune a wurin don har saida taga magrib ta tafi zuwa dakinsu

Sallahr magrib tayi bayan tagama ta nufi part din Imad ganin taji sauki don haka bari yau ta koma bakin aikinta

Kitchen ta shiga ba sallama ba komai zubaida datake bakin kofa sakalau tayi da baki tana kallon Hurriya wadda bazaka ce mata yar aiki bace yadda tayi wani irin kyau kuma sai kamshi takeyi zubaida bakin ciki ne ya turniketa don bata manta yadda uban gidanta da Hamdan suka shiga damuwar rashinta ba

Ta tsani Hurriyar nan don batada mutunci ko kadan gashi duk inda taje ita ake kallo duk sauran mutanen dake zaune sun zama banzaye indai tana wuri haka ko su Hamdan basu tabayi mata magana ba karewa ko maganar Imad bata tabaji ba Amman ga yarinya da tazo jiya jiya tafi ta matsayi abun gaskiya yana matukar bata mata rai Amman zatayi maganinta very soon don ba zata zuba mata ido ba

Duk aranta take wannan sake saken

Baba RaBI ce ta kalli Hurriya tace ya jiki kinsha ciwo ko daga yanayin maganar ta zakasan ba har cikin ranta tayi maganar ba jiran amsar Hurriya take saida tana juyowa taga batanan Dariya suka saki Dukansu yan kitchen din shiru baba rabi tayi sannan ta daure fuska

Store ta shiga ta debo basmati tayi continental rice sai vegetables spaghetti wadda taji namomi sai kamshi take kowa kallonta yake amman ita kamar batasan anayi ba saboda earpiece ne ma makale a kunnenta

Saida ta gama suka jera trays din akace su shiga sukai masu ba musu Hurriya tabi bayansu da nata tray din

Basu tarar dasu a falo na farko ko a parlour na biyu basu nan sai a parlon na uku inda suka shiga kansu duk a kasa

Hurriya kallo daya tayi masu ta dauke kanta suka shiga jera abincin

Saidai tanajin idanun dake binta

Ludo sukeyi Dukansu su shiddan kallo daya zakayi masu kasan suna cikin farin ciki kuma suna enjoying game din Hamdan ne yake kokarin cinye game din Neela kuma kiri kiri taki bashi dama

Tunda Hurriya ta shigo Imad yasan ta shigo don lokacin data juyo ta kallesu with distaste yana kallonta saidai bata lura dashi ba shidai yana mamakin halinta na iko da raini wayau Because he never came across someone like her ba all his entire life  komai nata ya bambamta bata tsoron kowa acikinsu abinda takeso shi takeyi yasan tana aiki yanda ya kamata indai ta fannin aiki ne baza a kamata da laifi ko ha'inci ba

Bata gaishe da kowa sannan bata kula kowa he can't read her duk yanda yaso ya dan fahimce ta ya kasa saboda ta rufe kowace kofa da dan mutum zai iya karantar ta

Saidai akwai abinda har yanzu yake bude wanda ta kasa rufe shi duka she's lonely saidai kallo daya idan kayi mata baza ka gane kadaicin dake tattare da ita ba saboda yadda ta rufeshi ta ko ina

Liya ce ta kallesu tace please Quit the game for now your food is ready Ammar ne yayi saurin tashi yace daman yunwa nikeji  ya nufo din dining su Hamdan da amrah suka biyo baya kowa yaja kujerar shi ya zauna

Neela ce tazo ta zauna sannan Imad ne karshe Ammar ne ya dago zaiyi magana aiko cikin sa'a idonshi akan na Hurriya wadda itama shi take kallo tana karantar shi saidai he looks very familiar to her kamar tasanshi kallon imad tayi wanda ya zauna a wani miskilance ya lumshe ido yanajin saukar idonta masu kaifi shima kallonshi tayi Dukansu tasansu amman A ina?Ganin idan fa tanason tagano inda tasansu sai ta koma duniyar tunani wadda batasan hakan kwata kwata

Ammar dariya yayi yace Hurry ya jiki please come and join us

Hamdan yanajin ance hurry yayi saurin dagowa kamar hadin baki Dukansu suka rinka kallonta Amrah ce ta taso tazo wurin Hurriya wanda ta kasa boye murnarta alamun zata rungume Hurriya tayi saurin ja baya sannan tace kada ki tabani idan ba haka ba marinki zanyi daga mata kai amrah tayi stiill tana farin cikin ganinta

Bude baki kowa yayi don jin furucin Hurriya na zata mari amrah saidai ba wanda yace kala saboda sunsan halin amrah indai akan abun da takeso ne yanzu ko maganar banza idan sukayi ma Hurriya to ba wanda zai kwana lafiya don idan ta farayi masu rigima da kuka to sai Allah

Bude bakinta amrah tayi sannan tace Hurry please grant me a wish tana daga mata hannu alamar don Allah ta taimaka mata shiru Hurriya tayi ganin tayi shiru amrah sai tayi tunanin kilan Hurriya batajin turanci sai tace don Allah kiyiman abu daya

Hurriya frowning brows dinta tayi ta kalleta mockingly tace mi kikeso dariya Amrah tayi tace don Allah muci abinci tare shiru wurin yayi kowa na jiran amsarta Ammar ne yayi breaking silent  din ta hanyar cewa haba yar mai kyau please join us yana karya murya hade da kanne mata ido kamar mace trying to look funny Hurriya gyara tsayuwarta tayi sannan tace you Better stop acting that way if not I promise you'll be a transgender by tomorrow morning saboda ka koma kamar wata amarachi Dariya kowa ya dauka shikanshi Imad duk yanda yaso kada yayi dariya saida ya dara

Neela a ranta take maganar muryar Hurriya ta hadu ba karya don wani accent mai matukar dadi take amfani dashi wurin magana Ammar ba karamin dadi yaji ba yadda tayi mashi magana don bai tsammaci hakan ba don yarinya ya lura bata magana kwata kwata don idan bakayi dagaske ba zakayi tunanin bebiya ce .

Hurriya zagayowa tayi taja kujera ta zauna kowa serving abincin shi yayi

Serving ta farayi ahankali don komai ahankali ta zuba tundaga kan appetize komai nata accordling takeyinshi cikin tsari ba wanda bai kalli yadda ta fara cin abincinta ba don da appetizer ta fara sannan taci kadan shima main dish kadan taci yadda zata  ida cin komai don a doka tun suna kanana ake koya masu table manners don shine yake determining they are from royalties kuma not an ordinary royal family

Don haka they've to be always mindful of their table manners duk wanda yaga yadda take cin abinci yasan she's from an elegant family because he the way she held her spoon ba kowa ya iya irinshi ba

Ganin almost all of them are staring at her plate ya sanya a hankali tace bloody hell what am I doing cikin wayau da dabara ta lalata plate din ta canza salon cin Abincin.

They ate in silence tana gamawa tasha ruwa sannan ta tashi kallonta Dukansu sukayi Hamdan ne yazo yasha gabanta sannan yace Hurriya we're not done talking zaki bani diyarkin?i like you wani irin kallon banza Hurriya tayi mashi Hamdan turo mata baki yayi yace please Hurriya banza tayi dashi ta kama gabanta.

Zubaida da suka gama kallon duka scenes din abinda ya faru bakin ciki kam zuciyar ta har kuna takeyi hmmm kawai take cewa cikin ranta

Hurriya kam tana komawa ana kiran sallahr magrib

Alwala tayi sannan tayi sallah bayan tagama ta nufi babban kitchen tareda crossing hannunta abayanta kallon yadda kowa yake hada hada tayi haule reza naganinta tazo wurinta saida ta kalleta tace yar nan naji ance kinsha ciwo Hurriya daga mata kai tayi

Kallon Haule reza tayi sannan tace aiki zamuyi zan biyaki haule najin kudi ta daga kai Hurriya bayani tayi mata yadda komai zai kasance

Sannan ta koma daki Bintu ta bama kudi ta siyo mata sabuwar reza da omo klin sai lemun tsami da gishiri kallonta Bintu tayi tana mamakin mi zatayi dasu saidai tasan kota tamabaye bata da amsa indai Hurriya ce don haka taje ta siyo mata duka abinda ta aiketa

Isha'i Hurriya tayi sannan ta sanya  earpiece a kunnenta tanabin waka Bintu tazo tayi mata saida safe sannan ta nufi makwancin ta

Saida dare yayi sannan haule reza tazo da kularta wadda ta juyo tafasaasun ruwan zafinta

Wurin Hurriya taje inda Hurriya take kwance don kamar ita take jira tanajin nishinta ta tashi

Haule reza ta kalleta tace muje Hurriya daga ita sai hijab ta tashi hannunta rike da abinda ta aiki Bintu suka nufi wurin wasila don da ita takeso afara Hurriya tsayawa tayi tana kallon yadda komai ya fara gudana duk yadda Hurriya ta fada ma haule reza haka ta fara gudanar da ayyukanta don saida ta  fara Gangarawa ta daura ma wasila kyale ta dode mata baki wanda tana tabata ta tashi daga Bacci tana zare ido saitin fuskarta wasila tazo ta kalla sannan ta kalli hurriya tace ayi anan? Hurriya girgiza kai tayi

Haka haule reza ta rinka tambayarta saida tazo kan kafafunta sannan Hurriya ta daga mata kai Hurriya matsowa tayi tanuna mata Daidai inda zata yanka wurare biyar ne wanda duk idan aka taba ma mutum shi akafa tohm sai Allah haule reza kallonta ta rinkayi tana kallon rashin tsoro da rashin tausayin dake cikin idonta

Wasila kam ihu ta rinkayi Amman sam baya fita kiyi mana inji Hurriya ba bata lokaci haule reza ta daura sabuwar reza mai matukar kaifi sannan taja wurin da karfin tsiya wani irin azababben ihu ta saki Amman to no avail saboda baya fita baba haule ta riketa

sannan Hurriya ta fasa klin dinta guda daya ta zuba mata shi wani irin uban kara ta saki  tana shure shure Hurriya murmushi tayi sannan ta barbada mata gishiri ta hada da matsa lemun tsami a ciwon

Saida ta sanya haule reza tayi mata yanka biyar sannan ta barbada mata ingredients dinta

Tun tana kuka har kukan ya daina fita ba imani kwata kwata tattare da Hurriya ta bude kular nan ta debo tafasassun ruwa ta watsa mata akafafunta duka biyun ai wasila suma tayi

Haule reza kallon irin launin azabar da Hurriya take mata tayi tana mamakin rashin tsoro da rashin imanin yarinyar nan. Ta tabbata zuwa gobe kafarta tayi mummunar konewa .

Haka Hurriya ta rinka binsu saida ta tabbata duka tayi masu azaba iri daya don duk saida haule ta daure masu baki sannan tayi masu yanka biyar biyar Hurriya ta zuba masu  omo hade da gishiri da lemun tsami sannan ta kona kafafun da ruwan zafi

Bayan sun gama tace a a aske ma Hansa'u gashin kanta tass ita kuma wasila da Barira har yanzu tana binsu bashi ta wuce ta nufi makwancinta

Haule reza kallon bayanta tayi yadda take tafiya kamar tana tausayin kasa haka take takawa tunda take bata taba ganin mutum marar imanin Hurriya ba

Duk ihun da suke da neman ceton rai da suke ko dar bare gizau haka Hurriya ta rinkayi masu launin azaba  don tasan ba wanda bai suma ba acikinsu

Tabb inji haule tace akwai kallo dai wurin nan saidai sune suka ja ma kansu daman ance in kasa wata ba kasan wataba.

Hello fans yanzu zan rinka posting from Monday to Thursday saidai daga Friday zuwa Sunday ba post

Idan kuma kun fiso a rinka skipping rana daya tohm I will be waiting for your opinions

Love xoxo❤️👼🏽

[12/02, 4:54 PM] Khadyn Sp: 🌚Masarautar Qamar

A story about a mysterious palace

By Khadija (KMU)

27&28

Kwanciya tayi Hurriya tareda sauke ajiyar zuciya don yanzu ne zata iya Bacci cikin dadi don idan batayi masu hukunci ba gaskiya ba sunanta Hurriya Faisait Hamood ba.

Haule reza kam tana mamakin inda yarinyar nan ta samo kalar launin azabar datayi masu don bata taba ganin hakan ba saidai fa ba karya Hurriya muguwa ce tace sannan ta nufi makwancinta

Yau da safe da aka tashi aka iske duka yan click dinsu Barira suna jinya don kusan ihun wasila ya tadasu don azaba ta ko ina takeji kuka kam yinshi take kawai don a halin da take ciki da za'a cire kafar to da tanaso indai har zata rabu da ciwon da takeji.

Barira kam har garin Allah ya waye itada suwaiba to asume suke  saida aka samu da kyar suka farfado irin ciwo daya ne Dukansu suke fama dashi Dukansu saidai kowa na mamakin wanda yayi masu wannan danyan aikin

Hurriya yau ta samu ta tashi da wuri don har sallahr asuba ta samu damar yinta da wuri. Tanajin sai jaje akeyi Bintu ce tazo da gudu tana haki ta kalli Hurriya sannan tace naji abinda ya faru gasu barira Amman don Allah kece?kice bake bace don Allah kice man haka Hurriya kallonta tayi sannan tace nice Bintu And idan suka kara koda hararata abun da zanyi masu sai yafi wannan Bintu kallon Hurriya tayi sannan tace haba Hurriya miyasa zakiyi haka kinga kafafunsu idan kika gani sai sun baki tausayi wallahi dama kin kyalesu sunje da halinsu tunda yanzu suma zasu ce zasu rama kema zaki ce zaki rama kuma ance sarkin yawa yafi sarkin karfi kuma ma kinsan kaura saurayin barira ne sai ance shaho saurayin Hansa'u ne

Bintu batasan duk maganar da takeyi Hurriya tayi tafiyarta

Juyawar da zatayi  taga ba Hurriya saidai ganin inuwar Hurriya tayi

Hurriya tana fitowa saiga hauke reza wadda ta taya danyan aikin jiya

Kallon Hurriya tayi tana washe baki sannan tace Hurriya naga sako nagode kuma don Allah inson kibani dama  yadda idon akace gobe su kara to bazasu kara ba

Hurriya shiru tayi mata har tagama babatunta batace komai ba

Kitchen taje inna hanne na kallonta tazo tace Hurriya an tashi naji danyan aikin da kika aikata baki kyauta ba

Hurriya dage girarta tayi tace banzo don inji kyautawa da rashin kyautawa wurin ki ba malama ki zuba min ruwan zafi in kama gabana

Inna Hanne kallonta take kamar statue zata iya cewa tunda Hurriya ta tashi daga rashin lafiya to yaune ta samu jin muryarta mai tsayi har haka inna hanne wadda tayi curr tana kallonta tsarki ya tabbata ga Allah sannan tace lallai kedin gimbiya ce duk aranta take maganar don kwata kwata bataji haushi ba

Inna Hanne daukar bokitin tayi ta zubo mata ruwan zafi suka jero tare inna hanne rike da ruwan Hurriya kuma rike da kayan wankanta har suka zo toilet

Hurriya wanka ta shiga tayi sannan ta fito ta nufi daki

Sai kallonta akeyi don ba inda maganar bataje ba ita tayi masu Hansa'u wannan hukuncin wasu ta burgesu wasu kuma ta basu tausayi wasu kuma zaginta kawai sukeyi but who cares

Shiryawa tayi cikin uniform dinta wadanda sukayi mata kyau Sosai

Comb ta dauka ta tsaga kanta hudu sannan tayi kalaba manya manya guda hudu wanda suka sauka har gadon bayanta nade gashin tayi har saida ya dawo Daidai keyarta sannan ta fesa turarenta ta fita

Sashen imad ta fara zuwa aikam cikin sa'a ta gyara ko ina har dayan dakin shi wanda yake bacci

Tanajin karar ruwa hakan ya tabattar mata da yana toilet don haka tana gama mopping ta fito ta wuce part din zinariya wanda tunda ta fara aiki bata taba gifta kofar data wuce ta kitchen ba

Don haka tana zuwa tayi wanke wanke sannan ta fara hada breakfast tanajinsu suna gulma murya can kasa kasa Amman sautim maganar su radam a kunnen Hurriya wata a cikin kuyangin ce tace hmmm labari da dumi duminsa fa

Kowa cewa yayi munajinki subira ta kusa dawowa fa ance sati mai zuwa zata dawo, wata acikinsu ta fara salati tana jajanta masu subira fa suna cikin matsala ta dade batazo kasar nan ba don haka dayawa kilan sun manta wacece subira AI kuma ba lallai kowa ya iya manta subira ba saboda irin record din da ta bari

Hurriya duk tanajinsu wata acikinsu tace shekara fa ta kusa zagayowa shiru Dukansu sukayi suna zare ido wata acikinsu tace nidai bani da kyaun da za'a rasani a masarautar nan

Jakadiyar zinariya ce ta shigo ta kallesu tace me kukeyi ku wuce ku kai abincin Dukansu daga mata kai sukayi itadai Hurriya na aikinta

Tana gama aikin ta fita ta nufi inda suke wanki tana zuwa ta iske wasba tana wasa da dan icce tana ganin Hurriya wasba ta saki iccen ta rugo wurinta tana dariya  tace tun dazu nike jiranki Hurriya bata ko kalleta ba tayi gaba inda ta saba wanki

Kayan ta fara wankewa wasba kam ta samu wuri kusada Hurriya ta zauna tana ta bama Hurriya tatsuniya mai ban dariya duk intayi sai taga Hurriya fuskarta daure sai tace bari in canza haka wasba ta zauna tana bama Hurriya labarai masu ban dariya Amman Hurriya ko murmushi batayi ba bare dariya

Wasba kuma taki tafiya sai can wani yaro yazo ya kirata ance ana kiranta tashi tayi  ta ruga tana tsalle ta juyo tayi ma Hurriya alama da hannu Inasonki

Hurriya tsoki tayi ta cigaba da wankinta tana waka

Yunwa ce ta fara galabaitar da Hurriya saboda tun tashinta yau bataci abinci ba don haka tana ida shanya kayan ta nufo dakinsu

Harabar wurin tagani tasan cewar ba lafiya ba don haka ba tare da bata lokaci ba kutso wurin

Kowa ita yake jira a taron mutanen da akayi ta riga tasan da haka bata damu ba taja kai tana niyyar shiga wurin shaho ne ya tare hanyar yana watsa mata idanunshi masu firgita ma mutane lissafi itama kalloshi tayi tare da tsirtar da miyau a kafarshi tace disgusting kaura ne yazo a 360 don ranshi yana matukar tafarfasa da wannan makirar yarinya mai kyau sai kace ita tayi kanta duk masarautar nan waye ya isa ya taba barirarshi ya kwana lafiya babushi

Sai ita ta watsa mata tuwo a fuska gashi kuma tayi masu wani irin salon launin azaba tabbas yau sai ya wulakanta

cikin zafin nama kaura ya daga dorinar shi zai zuba mata Hurriya da yau itama ranta yagama baci don bazata iya tuna when last tayi irin bacin ran nan ba ta rike dorinar da karfi tanayi mashi matsiyacin kallo wanda ke dauke da tsantsar mulki da kuma izza tace the moment you beat me with your filthy hands you're going to be executed ta matso tana mashi whispering tace kana  kuskuren dukana to hukuncika kisa

Ta saki bulalar ta tsotsi bakinta cikin isa da mulki tace duk wanda bai fasa dukana ba acikin ku Amman ku tabbata duk wanda yayi gigin kara tabani a masarautar nan da sunan duka to sai ya amshi laifin shi na taba lafiyar Hurriya Faisait Hamood this is a promise and try me and see ta watsa masu wani wukantacen kallo tace jakuna daku matsiyata ta shige cikin dakin tana barin kowa baki bude

Kaura da shaho kam kamar wasu duwatsu haka sukayi don sungani à idanun yarinyar duk wanda ya kara tabata to kilan lahira zai bakunta yadda ta furta kisa kuma yadda ta nuna hukunci mai tsanani mutum zai amsa saidai tayi matukar kunyata su

Shiru Dukansu sukayi tareda juyawa suka tafi cike da borin kunya

Ikon Allah yan wurin kowa ya rinka fada to miyasa basu daketa ba mi tace masu har haka watsewa akayi kowa da alajabin wannan Hurriyar

Sa'ade da karime suna kallon komai sa'ade ce tace wallahi na tsani waccar shegiyar Hurriyar karime tayi wata dariya tace naki akeji amman ki bari zamu yi maganinta a masarautar nan tunda kowa ya gagara maganin shegiyar

Bintu ce ta gifto matsawa tayi saitin su tace kafin kuyi maganinta ni Zan sanya tayi maganin ku mutanen kawai tana kallon yadda suka zare ido alamun shakka dariya tayi ta shige ciki

Sallah ta iske Hurriya nayi Bintu kallon yadda take sallar kawai tayi ta girgiza kai ta zauna tana jiran tagama sallahr

Bayan ta sallame sallahr ta juyo ta kalli Bintu wadda take gyangyadi murmushi Hurriya tayi wanda batasan tayi shi ba don da sauri ta maidashi sannan tace Bintu Bintu adan firgice Bintu ta tashi Hurriya kallon katifa tayi sannan tayi ma Bintu alamu data kwanta

Ba musu Bintu ta kwanta wani irin bacccin gajiya ya dauketa murmushi Hurriya tayi sannan ta dauki wayarta da ta amso chargy dazu wurin haule reza

Bude wayar tayi wani tunani yazo mata da sauri ta cire tunanin waka ta kunna ta kishingida nesa da Bintu

Inna hanne ce tazo da plate da kula na abinci kallon Hurriya tayi da ta lumshe ido tanajin waka sam batason wakar da Hurriya keji don akwai abubuwa da yawa gabanta karatun AlQur'ani ya kamata ta rinka ji ba waka ba Amman Hurriya is not helping matters

Murmushi tayi ganin yadda take bin wakar

Inna hanne tace Hurriya Hurriya saida inna hanne ta daga murya Sosai Hurriya ta tashi kallonta tayi ta dage mata gira alamun lafiya shigowa tayi tare da ajiye kular sannan tace abinci na kawo maki daga mata kai Hurriya tayi sannan ta koma ta kwanta ta dade bata motsa ba don har inna hanne ta tafi idonta rufe

Saida taji yunwa na damunta Sosai sannan ta bude idonta tare da cizon lebenta ta sauko ta zuba shinkafa da mai da yaji hada maggi mai tauraro

Kamar tanajin tausayin cikinta haka ta fara cin abinci har saida taji ta koshi sannan ta ajiye cokalin tasha Ruwa

Yau ya kama wata daya kenan da kona masu su barira da Hurriya tayi su kuma su shaho da kaura tunda Hurriya tayi masu warning dinan basu kara zuwa ba Amman sun kudirta aransu abinda zasuyi mata mai muni ne

Bintu kam da Hurriya sun zama tamkar yan uwa don Hurriya har ta fara bude mata wasu abubuwan duk da she's not allowed to do that saboda she's not to trust anybody in this life saidai mi after all she's human being too tana amsa sunanta yar adam don haka itama tanada émotions kamar kowa kawai ta iya boye émotions din nata saboda emotions dinta babbar barazana ce a rayuwarta bata yadda ace wani Abu yafi karfinta ba tunda ita har takeda kanta so she have full control of herself don haka she control everything  around her herself her maids kowa da kowa saidai yanzu kanta kadai zata iya controlling

Bintu ba karamin son Hurriya take ba don ita kadai take kallo taji sanyi a rayuwarta ko kuma ince a masarautar Qamar bata da kowa sai Allah sai Hurriya

Ita kanta Hurriya idan har kasan mi kakeyi yadda take kallon Bintu kadai zai nuna maka tana matukar tsantsar Qaunarta don idonta har wani gleaming na pure love yakeyi

Yanzu haka ma Bintu ce ta siyo masu awara da rake itada Hurriya

Zaune suke saman wani dakali su biyu Hurriya ba dankwali a kanta gashin kanta duka ya zuba a gadon bayanta don bata daureshi ba

Kallon wurin da wasba ke zama tana wasa da icce Hurriya tayi kafin ta sanya hannu cikin awarar wadda ta tauna sai kuma tayi murmushi wanda duka dimples dinta suka lotsa dan gleam din dake a

gefen idonta ya kara fitowa Bintu lahaula wala Quwatta illah billah kawai take ambato Lallai babu karfi da iko sai gurin Allah wanda yayi hallitar nan ba tare da makusa ba ita Hurriya wani irin kyau ne take dashi har haka?

Shin gwara da ya kasance bata dariya da ace tana dariya tabbas da dariyar ta zamar mata babban kalubale a rayuwarta acikin masarautar wani irin kyau take gani kota Ina gaban Bintu banda faduwa ba abinda yakeyi ita mace ma kenan wai tohm inaga namiji

Hurriya ta dage girarta daya ta kalli Bintu sannan tace kallon na miye?

Ba komai inji Bintu kasa rikewa Bintu tayi don da farko batayi niyyar fadar abinda ke cikin ranta ba cewa tayi MashaAllah Hurriya kina da kyau Hurriya batace mata komai ba ta kara sanya a wara a bakinta.

[12/02, 4:54 PM] Khadyn Sp: 🌚Masarautar Qamar

A story about a mysterious palace

By Khadija (KMU)

29&30

Saida taci awarar kusan guda hudu sannan tasha raken wanda aka daddatsa guda biyu

Bata Qara cema Bintu komai ba ta sauko Bintu nagani Hurriya ta fara tafiya itama ta sauko tana cewa Hurriya jirani banza Hurriya tayi da ita aiko Bintu ta rugo ta samu suka jera tare tana haki

Tana shiga aka fara kiran Sallahr magriba sallah sukayi sai ga inna hanne ta shigo wadda yanzu Hurriya na bata amsa yanzu idan tayi mata magana kallonsu tayi Dukansu Hurriya nagama sallah ta linke hijab sannan ta dauki wayarta ta makala earpiece inna hanne tace Hurriya kidan rufe kanki don Allah tunda dare yayi kinji

Ko kallon inda take Hurriya batayi bare tasan ran amsa ta fita zuwa part din Imad

Ba inda ta tsaya sai part din Imad wanda zasuyi tafiya gobe kuma yace mata tare zasuyi parking she must come

Ba kowa parlon don haka ba inda ta tsaya sai bedroom dinshi yana zaune ya mike kafafunshi yana amfani da MacBook sai Qamshi dakin yake na turaren wuta mai sanyin dadi

Lumshe ido Hurriya tayi sannan ta bude idonta masu kyau ta tsotsi lebenta

Batace mashi komai ba ta bude duka wadropes dinshi akwai wani wuri dake da jerin tarin designers suitcase, Daya daga ciki ta dauka mai matukar kyau da tsada na Bottega veneta ta ajiyeshi sannan ta fara shirya mashi kaya tunda ta shigo yake kallonta ta karkashin ido don ba karamin kyau tayi mashi ba kallon doguwar sumarta yakeyi  sai kafafunta da suke waje don rigar da ta sanya tsaga gareta sosai

A ranshi yake tambayar kanshi who is this mysterious girl wadda take neman  dagula mashi lissafi ji wata seductive shiga da tayi wadda duk wanda ya kalleta sai yaji wani abi tunda ga kanshi har zuwa tafukan hannunshi

Don yanzu yafi kowa sanin Hurriya da zai iya cewa dagangan takeyi saboda tayi seducing dinshi ko kuma ta ya kulata

Tunawa yayi ko kallo na biyu batayi mashi bare har ta kasa dauke idonta daga gareshi don ko gaisheshi batayi ba wani dogon conversation din da ya taba shiga tsakaninsu bare harma yace donshi takeyi

she's so unique and classy may that's why he started to like her

Hurriya tanajin idonshi akanta murmushi tayi sannan ta cigaba da hada mashi kayanshi

kaya take shiyar mashi masu matukar tsada da kyau kallon yadda take komai yake yi

Hurriya tunanin da batasan tayi saida tayishi dan the more tana kallon su Imad da Ammar take ganin tasansu and the most funniest thing ever shine  tagano imad dasu Ammar maternal cousins dinta ne mamansu da babanta uwarsu daya ubansu daya they used to come too their palace lokacin suna yara

Ammar and Imad are her best friends kuma sune favorite cousins dinta ba kamar Imad saboda lokacin they don't get along but deep down she was his favorite person itama Hurriya haka yake a wurinta she used to annoyed him har sai ta tabbatar da ta sanya shi kuka tukuna saboda zuciya gareshi idan tayi mashi abu saboda bacin rai shi kuka yake Bata iya kirga yadda takesa shi kuka sai kuma ta dawo tana bashi hakuri Ammar yayi ta yi masu dariya

She doesn't get along with the female twins duk da sune mate dinta Amman basa shiri saboda suna mata kallon mutum mai girman kai da nuna isa Because she's from Heral palace

Ita kuma Hurriya she doesn't care at all don ko da ace sun shige mata tohm zalintar su zatayi because alokacin Hurriya muguwa ce duk salon mugunta ta iyata mamansu itace favorite person dinta don tana matukar son Aunty Banafsha saidai tana shekara goma rabonta da su Imad da Aunty banafsha lokacin zataje Mexico akwai fashion school din da zatayi acan tohm kusan kowa saida yazo a yanuwanta sukayi bidding dinta farewell murmushi tayi tana tuna childhood dinta a hankali tace how times flies

Imad yanajin sautin murmushinta shima murmushin yayi daman tana dariya kodai he misheard her ne gaskiya baiji da kyau ba

Duk abinda Hurriya tasanya mashi mai kyau ne da tsada tunda yake bai taba ganin Mai great fashion sense dinta ba how did she know expensive abubuwa irin haka kuma tasan duk yadda kayan zasu bada ma'ana who is she?what is her identity?only God Knows sai kuma Hurriya din da kanta.

Bayan tagama ta zage komai sannan ta gyara komai ta juyo saitin Imad wanda ya kauda kanshi saboda kunyar data kamashi yana kallonta gyara murya yayi  sai ya rasa mi zaiyi ita kuma Hurriya taki ta daina kallonshi Dage girarta tayi sannan ta rungume hannayenta tace why are you staring at me kallonshi takeyi da idanunta masu kyau tana tsotsar lebanta imad shima gyara murya yayi yace wake kallonki yana dage gira daya harar shi tayi in an annoying way tace you manah sannan ta fita shiru Imad yayi yace kada fa ace wannan yarinyar ta rainani lallai ma I will Deal with her

Hurriya tana fitowa ta iske amrah da Hamdan sai ammar a balcony suna zazzaune

Ammar ne yace hurry ba gaisuwa banza tayi dashi ta cigaba da tafiya da sauri Hamdan da Amrah suka taso Amrah tayi saurin rike mata hannu Hurriya kallon Amrah tayi alamar ta saketa da sauri Amrah ta saki hannun Hurriya

tana rike kunne alamar tayi hakuri daga mata kai Hurriya tayi

Hamdan ne yace Hurriya Guess what?shiru tayi batace komai ba bata rai Hamdan yayi yace Hurriya you're not funny at all I won't share the story with you shrugging kafadarta tayi though tanason taji mi zai fada mata because she's starting to like the twins saidai mi batada lokacin batawa tafiyarta ta fara da sauri Hamdan yasha gabanta yana bata fuska dariya amrah ta farayi masu

Hamdan kallonta yayi sannan ya kara cewa guess what?ganin tayi banza dashi ya sanya yace tunda bazakiyi guessing ba ni bari na fada maki we're going to Ethiopia 🇪🇹 tomorrow In Sha Allah Gaban Hurriya ne ya fadi don batasan inda zasuje ba sai yanzu da yake fada mata ta dai san gobe zasuyi tafiya Ahankali batare da tasan maganar ta fito ba tace ethopia daga mata kai yayi sannan yace mata eh manah Do you want to know why I was so happy ? Daga mashi kai tayi alamar ehhh murmushi yayi yace I will get to see Layla Khasheem she's my cousin all this while bansaniba sai ba'a dade ba fa Ammar yake fadamin suka barni inata hauka ashe yar uwata ce ma it will be my first time to be in

Heral palace I can't wait oo har na kosa naga yanda masarautar take don labarinta da ake bani na kasa yadda akwai masarauta irin haka i will get to see it with my own eyes and zanga my grandparents sannan yayi dariya

Gaban Hurriya banda faduwa ba abinda yakeyi Heral palace can zasuje kenan gobe itafa? Heral palace nan ne fa asalinta nan ne gidanta Amman ta gagareta Because of abubuwan da suka faru

Shiru tayi wanda ta fada duniyar tunani past dinta iyayenta wanda batasan ta tuna komai da ya faru Amman ya zatayi karar hoton da tajine ya sanyata dawowa daga duniyar tunanin da take neman fadawa kallon Hamdan da wayar dake hannunshi kirar iPhone 14proMax tayi inda ya dauki hotonta shida ita Hamdan yace idan mun isa i will tell Layle Khasheem about you sai in nuna mata picture dinki taga yanda kuke kama Da wani irin bacin rai Hurriya ta amshe wayar tareda yadda ta kasa Qarar fashewarta kawai akeji

Idonta har ya canza launi saboda tsananin bacin rai Hamdan shima ranshi ne ya fara baci don shima badai zuciya ba kallonta yayi da muryarshi wadda bata wasa ba yace Hurriya how dare you yana mata wani banza kallo itama kallon takeyi mashi tace And how dared you took a picture of me without my consent kallonta Hamdan yayi wanda yake nuna tsantsar bacin rai yace what did you think of yourself girl you're nothing here but just a filthy maid me kika dauki kanki bari kiji in fada maki ma if You're feeling great you're not great don kinga anayi maki magana ba komai ya sanya ake maki magana ba saboda kinyi man kama da Layla Khasheem isn't it something great a whole prince took a picture of à fouling smell maid like you bari kiji you stink and you're disgusting kuma kedin ba komai bace face kaskantaciyar baiwa wadda ta fito daga tsatson kaskantattu mutane shas bai ida fada mata kalmar shasha ba yaji saukar maruka guda biyu a tare bai ida juyowa ba ya karajin ta sakar mashi lafiyayyen maruka biyu kara daga hannunta tayi ta kara sauke mai wani marin tana kallonshi da idanunta da suka kada sukayi jawur kamar an zuba mata barkono muryarta har wani shakewa take saboda bacin rai tace And who are you to say that Hamdan shima muryar shi ba dadi yace how dared you slapped a prince with your stinky hands ya nufota alamar zai mareta Amrah ce tayi saurin rikeshi tace haba Manah Hamdan calm down stop please miye haka Ammar ne yazo wanda tun farkon abun yana kallon abinda ya faru duk da Hurriya ce bata da gaskiya Amman sam Hamdan bai kamata yayi mata irin rashin kunyar nan ba kuma ta wani fannin shima Hamdan baida gaskiya

Kallon Hurriya yayi tare da matsowa inda take da niyyar bata hakuri wata irin tsawa ta daka mashi looking so angry 😡 tace Ammar don't say a word here it's between me and Hamdan kuma wallahi sai yaji ajikinshi this is a promise gobe idan akace ya karayi ma wani rashin kunya bazai kara ba ta ida maganar da wani irin bacin rai ta kama gabanta

Hurriya har bata kallon gabanta how dare him take ta cewa how dare him har tazo dakinsu duniyar tana bata haushi

Hamdan kam wata irin ajiyar zuciya ya saki sai kuma ya fashe da kuka tare da rungume Ammar yace inna lillahi wa'inna ilaihi raji'un Ammar what did i did na kwafsa did i just yell at her wani kukan ya kara saki yace zaginta fa nayi da iyayenta na bani ya zanyi idan Hurriya ta daina kulani i just like her why? Amrah da takejin conversation dinsu ta harareshi in a disgusting way tayi tafiyarta ta barsu

"Ammar patting bayan shi ya rinkayi yace it's okay kadaina kuka kada ka damu zatayi hakuri" a hankali ammar ya rinka kwantar mashi da hankali tare da yi mashi alkawarin zasu bama hurriya hakuri gobe kafin su tafi daga mashi kai kawai ya rinkayi har ya samu ya lallashe ya rakashi chamber dinshi

Hurriya ba abinda tayi face kwanciya  tare da lumshe idonta duka abinda ya faru na dawo mata hakan da tayi shine Daidai idan har ya nuna ma wani ilta acikin Heral tohm tabbas she will be at risk rayuwarta zata kasance cikin hadari

Mutane iri biyu ke nemanta da masoysnt da kuma makiyanta kuma ita kam batasan kowa yaganta a cikinsu she will wander around the world she will be freed from all those fights of powers zata tsaya a masarautar Qamar har taga yadda Allah zaiyi da ita

Yau ta kama su hamdan zasu tafi duka ma'aikatansu da dogarawa da kuyangu ba wanda bai masu rakiya ba zuwa airport ba

Neela kam kallon kowa tayi tanason taga Hurriya ta ina zata bullo?saidai shiru bata ganta ba kallon Liya tayi sannan tace wai ina Hurriya Liya murmushi tayi tace I don't know

Imad shima sai kallon wurin yake yaga ta inda zata fito Amman bata ba alamar ta

Hamdan kam kamar yayi kuka saboda takaici gashi Amrah ta dauke mashi magana kwata kwata duk yanda yaso yayi magana da ita sai tayi banza dashi

Kallon kowa yayi saidai kwata kwata ba gifcin Hurriya kuka ya fashe dashi tareda rungume Ammar dake kusa da Hamdan Ammar lallashin shi kawai yake tare bashi hakuri yana yayi shiru

Announcement din da suka ji ne ya sanya su tashi wadanda suka yo masu rakiya suna dukar da kai Ammar riko Hamdan yayi sannan suka nufi jirgin

Ma'aikatan Saida suka tsaya  suka tashi sannan suka juya.

🌚Masarautar Qamar

Page 31&32

Karfe 3:44 jirginsu yayi landing tun a cikin airport din ake masu wata irin busa da algaita ga wasu mutane tsaye gigantic da wasu kaya da basu taba Ganin wasu irinsu ba

Durkusa masu kawai ake ana gaishesu Dukansu a

They're from the imperial family kenan inji wasu wadanda sukayi landing tare dasu Imad

Imad frowning fuskar su sukayi hade da takaicin wannan durkusawar da akeyi masu saboda islamically ba kyau Amman basuji ko an fada masu saboda basa practicing musuluncin sosai duk da cewar musulmai ne Amman abinda sukaga dama shi sukeyi ba tare da sanin sun aikata laifi ba

Amrah da Hamdan bude baki sukayi Ganin yadda akayi masu kneeling tare da dukar da kai Ammar tsoki yayi cikin ranshi sannan yace Raise sannan suka tashi tare da ce masu welcome

Wasu mahaukatan bakaken jeep ne akayi masu convoy dasu a kowace bayan motar an rubuta Heral palace motocin kusan guda ashirin sai farar limousine a tsakiya bude masu cikin limousine din akayi ana durkusa masu

Imad ya fara shiga su Hamdan suka biyo baya zama sukayi cikin motar wanda yake kamar wani parlo wani dim light blue da red yana kawowa sai kuma ya dauke Différents varieties of meals da small chops ne a cikin motar Liya ce ta lumshe ido tare da cewa Heral palace is freaking rich wannan motar itace latest limo of 2022 worthing shiru tayi tace gaskiya kudinsu yayi yawa .Neela tabe baki tayi tace aifa mun bani da extravagance life har sai an sanya mutum yaji baisan komawa masarautar Qamar

Imad baice komai ba Hamdan ba wani spirit tattare dashi don rungume da ammar yake kamar wani yaro

Basuci komai ba har suka iso Heral palace Din

Busa da algaitu ne akeyi kota ina Mutane kam basu da adadi kowa da irin abinda yakeyi

Hamdan da Amrah sakin baki sukayi suna kallon komai don All their life basu taba Ganin masarauta mai kyaun wannan ba everything is screaming rich and elegant tun daga kasan masarautar har sama

Daidai inda ake taron aka bude masu mota Dukansu suka fito sannan aka sanya ma kowanne acikinsu alkyabba mai matukar kyau da tsada banda kamshi ba abinda alkyabbar takeyi

Neela da Liya murmushi sukayi ganin yadda duk suka rikice da masarautar masarautar Heral kenan duk idan mutum ya dawo sai yaga canji bare wannan karan canjin da yawa sosai

Duk inda suka gifta durkusawa ake ana masu kirari har suka zo inda ya kamata su zauna ja masu kujera akayi

Basu dade ba aka fara annoucing shigowar sarki da matarshi kowa a wurin natsuwa yayi tare da sadda kai har saida sarki ya shigo tare da zama kallon saitin da suke yayi  murmushi sarki Hamood yayi ya tashi ya nufo inda suke hannun Hamdan ya kama tare da shafa kanshi murmushi yayi yana kallon kamanninshi da Banafsha Amrah ya kalla yace mata amarya ta Hamdan da Amrah sukayi sauri suka gaisheshi yadda suka ga yan masarautar nayi

Haka su Neela suka gaishe shi kallonsu yayi tare da yin murmushi a hankali yace Hurain itama yanzu tazama yan mata kamar su ya fada cikin ranshi murmushi yayi yanajin wani Abu aranshi saboda babu rana da zatazo ta wuce baiyi tunanin Hurain ba yana tunanin ko tana raye ko ta mutu Allah shi yabar ma kanshi sani don ba inda baisa a nemeta ba saidai Duk maganar Dayace babu ita babu alamunta

itace favorite jikarshi saboda tsananin mulkinta da izzarta kuma kamanninta shi ta dauko da mahaifiyar Faisait  wato bahiyya mikati shiyasa Allah ya jarabce shi da sonta yana fatan duk inda take Allah ya sanya tana lafiya sannan tana cin abinci

Muryar Imad ce ta dawo dashi daga tunanin da ya shiga sakin Hamdan da amrah yayi sannan ya rungume imad da Ammar

Yana tambayar su lafiya Dukansu suka amsa mashi lapia lau mutane wurin ba wanda idonshi ke kansu don kowa ya sadda kanshi matarshi kam kamar ta mutu saboda bakin ciki don ya manta da kowa dake wurin ba wanda yake ganin a wurin sai marayun jikokinshi.

Hurriya ta dade tana bacci yau saboda tasan su Ammar sun tafi dagangan taki rakasu Airpot din tasha baccinta yanzu tagama aikinta ta nufi wurin wanki saidai bata ida kai wurin wankin ba taji ana busa Algaita ana kida hayaniya ake kota ina Khalifa Qamar ake cewa Khalifa Qamar Khalifa Qamar Khalifa Qamar

Totsar bakinta Hurriya tayi tace Nonsense ta nufi wurin wankinta saidai maganar kawai takeji ana Khalifa Qamar ya dawo subira itama ta dawo salati taji anayi ana cewa wai daman Khalifa Qamar har yanzu yana a masarautar Qamar aiko muna cikin matsala don ance Khalifa Qamar makaho ne saidai baida mutunci  ko kadan  haka itama subira Hurriya tanajinsu saidai wankinta kawai ta cigaba dayi

Tunda tazo take mamakin rashin ganin wasba da ba tayi yau ba duk da batayima yarinyar magana amman tana enjoying company dinta sosai wankinta ta cigaba dayi tare da cire tunanin yarinyar a zuciyarta

Amman wata zuciyar na cewa taje ta dubata saboda hakan bata taba faruwa ba tsoki tayi ta cigaba da wankinta ta jima tana wanki kafin tagama ta koma daki dan ko sallah batayi ba saidai tana zuwa kwanciya tayi saidai hayaniya da kidan da akeyi shine ya hanata baccin da take so tayi kunnuwanta duk an cika matasu ba abinda takeji sai khalifa Qamar tsoki ta karayi tare da runtse idonta

Da wani irin gudun masifa convoy din motocin suke tafiya acikin masarautar kowani mahaluki ya matsa daga inda yasan zasu wuce don ko daga yadda kaga suna tafiya kasan shidin mai zafi ne

Busa da algaita kawai ke tashi wurin hade da sunanshi da ake ambata wato Khalifha Qamar

Motar tsakiya wadda take itace kadai iri daya a convoy din Roll Royce aka bude mashi inda yake zaune idonshi a rufe looking so mighty walking stick dinshi mai masifar kyau da daukar ido tafara saukowa kafin shima ya biyota baya sunanshi kawai ake ambata a wurin

A hankali ya fara tafiya mai dauke da mulki da izza don yadda yake tafiyar ko sarki albarka walking stick dinshi ta Brass cane wadda ta zama encrusted with Swarovski elements don Swarovski element na crystals din ba karamin taimaka ma sandar tayi wurin fiddo da tsantsar kyau da tsadar ta tayi ba the flamboyant design glittering Swarovski element crystal doesn't stop at the handle don ba a handle din sandar kawai ya tsaya ba don har kasan shaft din dauke take da glittering Swarovski element

Kallo daya zakayi ma handle din sandar da shaft dinta kasan cewar they are made from high quality brass wanda yake lullube da crystals yadda yake tafiya kadai zakasan lallai wannan jinin sarauta ne kuma sarautar a jikin shi take yawo ba haye yayi ba gado yayi ko fuskar shi babu alamun sauki bare rahma he's not young because he looks 36/37  he's huge and gigantic don Khalifha Qamar sunanshi Amman inda ya fito anfi  saninshi  da cobra blind snake saboda shidin kamar ba mutum yake ba saboda yadda yake he exude danger that is susceptible to a lifetime harm that leaves you wondering what is different about him that no other human being has.

He's intact kamar kowani mutum mai lafiya saidai his aura,peril and danger that always follow him behind wanda ba kowa yake da hakanba. a business world ana kiranshi da cobra blind snake saboda poisonous dinshi da danger dinshi a masarautar su kuma ana kiranshi da Khalifha Qamar

Tafiya yakeyi rike da sandar shi sai glasses din dake a fuskar shi wanda dan mutum bai isa ya hasko idonshi ba saboda makantar dake tattare dasu

Wucewa yake ta mutane kusan kowa yana durkusawa yana gaisheshi amman a wurin tamkar baisan dasu ba don ko kallo basu isheshi ba wani acikin security dinshi yazo wanda da alama kamar hakan dokace a wurin shi a hankali kallonshi yayi sannan ya kalli security's din yace they're all fired chief of security din ya sara mashi tara da bowing yace okay sir ya tafi